□□□□□□□□□□

FANSA

REVENGE

□□□□□□□□□□

Story en Written by dija waziri

I dedicated this page to you Xee yabo tnx for the love nd care Allah yabar mu tare ya kara had'a kanmu😘😘

AUDHU BILLAHIS SAMI'UL ALIM MINASH SHAITANIR RAJIM

BISMILLAHIR SHAMANIR RAHIM
Godiya ta tabbata ga Allah daya bani ikon rubuta wannan littafi yadda na fara lfy Allah kasa na kare shi lfy Allah yasa ku amfana da abun dake ciki

Kuskuren dake ciki Allah ka yafe min

Na gaisheku yan online Hausa writers nd walae/dija novel's , m sultan novel nd Wally novel

©(OHW)

January 2017

page

1&10

""Wasu yan mata nagani su uku,cikin wata black d'in mota tasha tenxac kiran BMW, biyu a gaba sai d'aya a baya wacce bazata wuce shekara 19 ba fara sol da ita, ta takure wuri d'aya, ga dukkan alamu y'ar aikin suce""

""Wani katafaren gida mansion naga sun shiga, Gidan yana da girma zubi da tsarin gidan kamar na turawa,Wurin parking space suka je sukayi parking,wurin motocine kawai a jere iri da kala, sunkai wurin guda 15 ko wanne plate number na motar an rubuta *ss tafida*""

""Fitowa sukayi d'aya daga cikin yan matan ne, naji ta kira wanan yar budurwan da ahlam d'auko kayan nan ki fito dasu kikai part d'in mummy,suka wuce suka barta wurin,tsayawa tayi ta kalli yawan kayan sannan taja tsaki, wlh Allah ya shirya ku, ku a rayuwar ku bakuso kuga mutun ya huta ko taya zan iya d'iban wa'annan kayan oho""

""kwashe kayan tayi nik'i nik'i tashiga dasu,
Wani dank'areren palour naga ta shiga,zubi da tsarin falon yayi,komai na falon green nd white ne, Wata dattijuwa nagani zaune wadda bazata wuce 46years ba,zaune ita da wata yar baby suna shan drinks suna kallon tom nd jerry,k'arasowa tayi, ta rissuna ta gaida matar, hajiya ina wuni barka da yamma, yawwa sannu ahlam har kun dawo ina su nabihan suke?
sun je sashen granny,
ok toh ahlam kiyi ta hakuri kinji nasan aiki yana miki yawa,amma nasa A'i ta samo min wata wadda zata ringa tayaki kinji, girgiza kai tayi alamar eh, yawwa yar albarka toh yanzu je kici abinci,idan kika d'an huta sai kizo kiwa kausar wanka ki gyara mata d'aki, toh kawai tace ta mike ta fita, dakin ta ta shiga tayi wanka tayo alola tafito ta tayar da sallah""

""Hajiya ce zaune a palour ita dasu nabiha, suna lisafa kud'in kayan auren ya fadil, wata yar tsohuwa ce tayi sallama tare da wata yar yarinya da bazata wuce 16years ba suka shigo suka zauna,A'a A'i sai yau tun yaushe nike ta jiranki shiru,
wlh hajiya d'iyatace ta samu k'aruwa,toh kuma babu mai zama a wurin ta shiyasa kikaji shiru, Allah sarki Allah ya raya tow ya hanya? Alhmdll,toh masha Allah,yawwa hajiya naji kince ba babba kike so sosai ba, wannan zatayi? ta nuna yarinyar da suka shigo tare, kai anya kuwa wannan zatayi, naga kamar ahlam ma tafita girma gsky bazata iya aikin ba saboda yana da yawa,amma kibar min ita akwai wata friend d'ina da take son yarinya,toh shikenan hajiya bari naje insha Allah ranar Monday za'a kawo miki wata,toh A'i nagode ga wannan ki hau mota ta mik'a mata 5k,a'a hajiya wannan irin d'awainiya haka,toh na gode Allah ya k'ara bud'i ameen ai ae babu komai""

""Mum ce tace yarinya meye sunan ki? Nawal ta fad'a, Wow suna mai dad'i shekarun ki nawa ? 16,wow toh yayi kyau yanzu zansa a kaiki gidan k'awata ki dinga mata aiki,ina zaki zauna ko? kai ta d'aga mata a lamar eh,kallon noor tayi da nabiha ku kaita gidan ambassador binta anjima zan mata waya na sanar da ita,turo baki nabiha tayi dama ita ta tsani ace tayi hurd'a da yan aiki, toh mum driver ya kaita mana, toh banga dama ba ku zaku kaita, turo baki tayi tasa kuka ta haye sama kamar wata yarinya,sakin baki mum tayi tana kallon ta, Allah ya kyauta yarinya kamar wata yar yaye ko kausar baza tayi abun da take ba noor ce tace hmm ai nabiha halin ta sai ita, toh Allah ya shirya ta mum ta fad'i tare da kiran sunan noor tashi ki kira ahlam ta kaita d'akin su kafin a kaita""

kaduna

""Wata bak'ar mata naga ta shiga wani arnen gida wanda ya gaji da had'uwa, kana zuwa daga saman get din gidan an rubuta welcome to judge muktar house, gida ne babba wanda keda part part har guda uku, kuma kowanne k'ato ne gidan mace d'ayace a ciki sai mijin ta sai yarsu wata budurwa da baza ta wuce shekaru 19 ba""

""Zaune suke dukkan su ukun, da judge muktar da matarsa hajiya rabi sai yar tasu mai suna malika,suna tattaunawa akan batun tafiyar malika abuja, sai ga matar tayi sallama ta shigo ta zauna suka gaisa judge muktar ne yace ladi yanzu mai ake ciki, kin gano mana mafitar yadda malika zatayi ta shiga gidan ss tafida? Eh toh a gsky judge muktar nayi iya bincike, nayi iya tunanina, naga babu hanyar da malika zatayi ta shiga gidan ss tafida saboda duk gidan matakan tsaro ne..... mafita d'aya ce malika sai dai taje a yar aikin gidan akwai wata mata dana sani wadda take kai masu yan aiki sai na mata magana, dafe k'irji judge muktar yayi aiki fa kika ce, ladi gsky ya'ta bazatayi aiki ba duk arzikina gsky a canja shawara,dafa Abi d'in nata tayi,Abi kayi hak'uri hakan shine kawai solution dazan iya shiga gidan ss tafida, naji zan iya jure duk abun da zan tarar, toh malika Allah ya baki sa'an abun da zaki jeyi, Ameen

Abi,ladi ki sanar da matar kinji ina so a wannan week d'in ace natafi malika ta fad'i tana shiren zama kusa da abi d'inta,
gyaran murya ladi tayi tace toh malika insha Allah zaki tafi a wannan week d'in,karki damu amma sai dai in zaki aje duk wani gayu da kike yi,wannan duk mai sauk'i ne ladi burina na ganni gidan ss tafida,toh ki shirya insha Allah jibi zanzo mu tafi sai na kai ki gidan matar dazaku tafi abujan tare ni yanzu zan wuce gida,
Ummi ce tace ok ladi mun gode da taimakon ki sai kinzo jibin, toh hajiya sai anjima alhaji sai jibin yawwa ladi mungode Allah ya kaimu alhaji ya fad'a""

2weeks later

""Malika ce keta shiri mum na gefen ta tana taya ta had'a kaya system d'inta, ta d'auko zata sa cikin ghana must go d'in da aka siyo mata ummi ce tace ke malika me kuma zakije kiyi da system? so kike su gane,
Kai ummi ae dole na tafi dashi ko kin manta duk wasu important abubuwana suna ciki ai bazan tab'a bari su gani ba,toh Malika Allah ya baki sa'a amma nikam ina tsoro wlh saboda kina da rawan kai,kar kije ki dinga musu rashin mutunci don ke ba hak'uri gareki ba kuma nasan bazaki jure wulak'anci ba,
Insha Allah mum bazan musu ba,zan jure duk wani rashin mutunci dazan fuskanta ai na lokaci kad'an ne,toh Allah yasa,yanzu tunda mun gama had'a kayan sai ki nemi wuri ki kwanta before safiya kinga sammako zakuyi ko,
toh ummi gud nyt i love you ta sumbaci goshin ta, nyt dear Allah ya tashemu lfy, sai data tabbata ta kwanta, sannan ta kashe mata light d'in room d'in ta fita""

""Washe gari ya kama Monday 7:00am, malika ta tashi ta shiga wanka tayi ta fito, ta shafa mai sannan ta d'auki jan janbaki tasa,ta d'auko wani t-shirt riga tasa da wani zani sai d'ankwalin adiko,tana cikin shirin sai ga ummi ta shigo tana kiran sunan ta malika ! Malika! k'arasa shigowa tayi tace au ashe ma harkin tashi kin shirya kinga ko yanda kayan suka miki kyau kamar ko yar k'auyen gaske,
tunda kin gama fito muje kici abinci ladi tazo ke kawai take jira,kai gsky tayi sauri wannan irin sammako haka, kinji yarinya bake kika ce tazo da wuri ba naga tun 6 kikace tazo don tazo 7 kuma sai ya zama wuri ni muje kici abinci kar ki tafi da yunwa,
a'a ni fa ummi a k'oshe nake banjin yunwa,toh yau kuma ai shikenan amma yanzu ko d'an tea baza kisha ba ? no ummi am ok banajin cin komai burina na ganni gidan ss tafida,oh ni rabi tun shekaran jiya kike magana d'aya toh Allah ya kaiku lafiya dai,
Ameen my lovely ummi shi yasa nake sonki saboda kina min addu'a mai kyau, toh naji ni dai yanzu fito mu tafi,sunzo fita kenan sai ga judge muktar shima ya fito yana kiran matarsa,
Rabi! Wai kiran malikar ne har yanzu fitowa sukayi tana Alhaji gamu nan fa ta tsaya shiri ne kallon malika yayi wow malika haka dama kayan hausawa ke miki kyau gsky kinyi kyau,ga wa'innan kisa cikin kaya karki manta dasu ya mik'a mata wasu cameras guda uku malika yau zaki tafi ina k'ara gargad'in ki akan kar kiyi wani abu dazai ja'a rufe ki ko yasa asirin ki ya tonu, insha Allah Abi bazan yi ba ae nasan me nake yi toh Allah ya kiyaye har mota suka rakasu sannan suka dawo""

""Gidan A'i suka nufa basu jima sosai ba suka isa a k'ofar gida suka tarar da ita tana shirin shiga napep, da sauri ladi ta k'wala mata kira, ai ki tsaya da Sauri ai ta k'arasa inda suke a tsaye a'a hajiya ladi gidanki fa nake da niyan zuwa naji kince 6 zaku zo kuma na jira naji shiru shine nace barin je naji lfy,lfy qlau wlh ai kawai dai

wani uzuri ne ya rik'e ni, ok toh tunda ta shirya ma barin d'auko kayana kawai mu wuce bara nawa d'an napep d'in magana, ladi ce da sauri ta tsaida ta a'a ai barshi kawai ya tafi na sauke ku tunda tare nake da drive, ok hajiya toh bara naje na d'auko jakata sai mu tafi ,ok toh muna jiran ki mota,
malika ce ta kalli ladi wai kina nufin park zamuje? Yes nan zamu,kinsan akace zaki tafi a motar gida akwai problem sosai, bakin ta sanye da chingum tana taunawa tace ok Allah ya kaimu lfy ,ladi ce tace ameen malika amma dai ina fatan zaki cire chingum d'inan kafin ku isa? Cikin rashin fahimta malika ta kalli ladi tace akan me zan cire bayan ina so?
bana so su miki kallon mara kunya, toh fa wata sabuwa inji yan caca toh wlh ladi bazan cire ba wato sukuma haka suke dan mutun zai zauna k'ark'ashin su toh ni bazan d'auki rainin hankali ba dama kawai nacewa su Abi zan jure duk wulak'ancin dazan fuskanta saboda su barni ne, bawai har zuci bane,murmushi ladi tayi ta dafa kafad'ar malika dama nasan kawai kin fad'a ne,amma nasan wacece ke tun kina k'arama bakya son raini amma kiyi a hankali duk da nasan baki da tsoro,suna cikin hiran sai ga A'i ta shigo, da sauri sukayi shiru da zancen da suke ,ladi ce tace A'i har kin dawo ne ? eh hajiya nadawo amin afuwa na dad'e sosai ,a'a babu komai muje ko,shiga motar sukayi suka d'auki hanyar tasha 10 minutes ne ya kaisu don dama basu da nisa sosai da tasha,sallama malika sukayi da ladi sannan suka shiga bus ,suka d'auki hanyar abuja""

""Tunda suka d'auki hanya malika ke barci ba ita ta farka ba sai da suka iso cikin garin abuja,a tasha suka sauka suka tsari mota suka d'auki hanyan maitama,
Dai dai dank'areren gidan ss tafida mai motar ya tsaya suka sauka, get d'in gidan suka sauka wanda ke kewaya da sojoji ,wani soja ne dake tsaye k'ofar shiga cikin gidan yayi checking d'insu before ya barsu suka shiga cikin gidan,nan ma matakan tsaro ne birjik a haraban gidan ,sakin baki malika tayi tare tare da mamakin irin yawan sojojin dake gidan nan ma sai da aka musu tambayoyi kafin aka kira hajiya aka sanar da ita sannan tace su shigo""

""malika dai bin ai take kawai har suka shiga cikin gidan wata yar tsohuwa suka gani zata wuce ai ta tsaida ta baba adama, juyowa tayi da sauri dan taga mai kiran sunan ta, a'a ai maraba lale sannu da zuwa ku shigo mana bara na kira miki hajiya d'azu ko ta gama maganar ki ashe dai kina tafe,wlh ina tafe ae bazan sab'a alk'awari ba mun riga munyi da ita yau indai ba wani uzuri ba babu abin dai hanani zuwa , hakan ma nada kyau ai kina k'okari sosai barin fad'a mata,ta wuce sama tabar su a falo zaune,
bata dad'e da sanar da hajiya ba ta sauko tazo ta samesu zaune kan carpet suna kallo malika duk ta had'e rai kamar wadda aka ma wani abu , hajiya ce tayi gyaran murya da yasa A'i ta dawo da hankalin ta kan hajiya da rawan jiki ta matso kusa da ita, hajiya amin afuwa wlh ban san kin zo ba ,da murmushi tace babu komai A'i ya hanya? lfy qlau haji yau kan nasan za'a dace, ina wannan zatayi ta tab'a malika,
sai a lkcn ta juyo ta kalli hajiya sannan ta gaida ta, da fara'a hajiya ta amsa tare da mamakin yarinyan don batayi kama da wacce ke shan wahala ba ,
A'i ce tace hajiya zatayi koh?d'aga mata kai tayi tana kallon malikar eh zatayi ai nagode, kai hajiya nifa bana son godiyar nan taki fa kin cancanci hakane,shiyasa duk abun da kike so nake miki kuma kina da tausayi baki da wulak'anci kinsan darajan mutum, nice da godiya bake ba,ni zan wuce amma zan dawo nan da wata uku, toh A'i Allah ya nuna mana ga wannan kiyi kud'in mota , kuma idan zaki wuce kiwa baba Adama magana na bata sugar da shinkafa ta baki, toh hajiya nagode Allah ya k'ara budi yasa kifi haka sai anjima ameen A'i toh sai kinzo , tashi tayi sukayi sallama da malika ta wuce""

""Hajiya ce ta kalli malika dake zaune gefe da kujeran ta, tace ya sunanki? sosa kai malika ta soma yi tana inda inda snn ta kalli hajiyan tace diyana , murmushi hajiya yi tace diyana kuma ke musulma ce?" tmbyn ce taji ya b'ata mata rai ,
fuska a tamke tace musulma ce ni , hajiya ta fuskanci maganar ta mata zafi da murmushi tace diyana naga kamar kinji haushin maganata ko sunan ne naji bai yi kama dana musulmai ba, murmushin yak'e tayi tace babu komai hajiya banji haushi ba""

"" Toh masha Allah a wani gari kike? a k'auyen kaduna nake ,eyya toh yanzu zaki ringa min aiki d'akin mijina zaki ringa gyarawa sai d'akina duk wani aiki daya shafi nashi toke zaki ringa yi kuma akwai falon bakin sa nan ma duk yana cikin aikin ki,

barin kira yarana su nuna miki, ita dai malika tow kawai take cewa tare da wani murmushin farin ciki, hajiya ce ta k'walawa ahlam kira da sauri ta amsa tare da barin abun da take tazo, tunda ta shigo take kallon malika har ta zauna tace hajiya gani,
yawwa ahlam jeki sama kice su nabiha suzo ina jiran su ,toh kawai tace tana kallon malika har ta haye sama,
bata jima sosai ba tadawo tace wai suna zuwa, nabiha ce tazo da gudu noor biye da ita tana binta, fad'awa tayi jikin mum tace mum kinga sis noor ko , hankad'ata mum tayi ni tashi a jikina kunfi kusa tunzura baki tayi ta zauna tana kallon malika ,noor ce tace mum wanan fa?" Yawwa noor zoki nuna mata dakin dad dinku da nawa da duk inda kika san ya shafi na dad dinku ita ce now nanny din dad dinku, kallon ta noor tayi da mamaki don kwata kwata batayi kama da yan aiki ba tace tashi muje ko ya sunan ki fuska a yamutse malika tace diyana kallon mum nabiha tayi tace diyana kuma ?" da sauri noor taja malika suka bar falon don tasan nabiha zatayi rashin mutunci,

nabiha ce tace mum arniya ce zata ringa wa dad aiki tab lalle akwai matsala , mum ce ta d'aga mata hannu ke dakata wayace miki arniya ce ko don kinji ance diyana,toh kar naji kar na gani don nasan halin ki musulma ce, toh fa dama musulmai ana samusu sunan arna?" eh gashi ko kin gani, yamutse fuska nabiha tayi tace mum wlh ko kama da masu aiki batayi ba ,kai nabiha kina da surutu bakin ki bata zama shiru ni tashi ki dubamin kausar kota tashi.....

WANENE SS TAFIDA

Ku biyoni don jin cigaban labari.....

Sai naji comment d'inku zan cigaba.....

Nice dai taku a kullum mai kaunar ku khadija waziri...😍😍😍😍😍😍😍

Edited by Zee Yabour
□□□□□□□□□

FANSA

REVENGE

□□□□□□□□□

Story /writing by dijawaziri

I dedicated this page to you mummy sultan and waliawaziri nd all writers

Page

11&15

©(OHW)

January 2017

WANENE SS TAFIDA

""Ss tafida shararren d'an siyasa ne, mai ji da dukiya, asalin sunan sa Alhaji sulaiman salisu tafida shine ake kiran shi da Ss tafida ya samo sunan ne tun yana k'arami abokan sa a school suke kiran shi da haka,shine kawai sunan ya bishi har girma

Yana da mata guda d'aya mai suna khadija hajiya khadija cikakkiyar y'ar kasuwa ce, bata cika zama sosai a gida ba, suna da yara guda 5 hud'u mata d'aya na miji sai cousin brother d'insu mai suna fadil,
Fatima itace babbar d'iyar ss tafida tana saudiya tana aure sai fahad mai binta shi kuma yana ingala yana masters d'inshi sai noor ita ke binshi sai nabiha su kuma suna neal universty dake garin abuja sai autarsu kausar wadda keda shekara 3""

""Ss tafida yana da k'azamin kudi don shi kanshi bazai iya lissafa irin dukiyar shi ba yana da kamfanin guda biyu da ake jakunkuna masu kyau da tsada a kogi state snn yana da kamfanin da ake wayoyi a dubai snn ana kawo masa motoci yana saidawa yana kuma da gidajen mai na kanshi guda uku d'aya a bauchi d'aya a kaduna d'aya a nasarawa state""

""Ss tafida yayi governor yayi sanata shekarun baya da suka wuce yanzu yana neman shugaban k'asa
Kuma ya tsani talaka baya son talaka ko na minti d'aya
tow readers kunji ko wanene ss tafida ku biyoni gaba zakuji ko wacece malika nd ambassador Binta""

""Malika ce zaune a d'akin da aka bata ita kad'ai ce ba'a had'ata da kowa ba kayan ta ta soma cirewa a cikin gana masgo d'in ta tana jerawa cikin wardrobe wani book d'an karami naga ta d'auko tayi ticking da red biro tana wani shu'umin murmushi,

"""Jin k'aran bude k'ofa tayi sauri ta rufe book d'in tasa a wadrobe, Asabe tagani mai girkin gidan ta shigo rik'e da abinci a hannun ta, da murmushi malika ta k'araso ta kar6i abincin tare da cewa dakin bari na zo na d'auka da kaina,a'a babu komai Diyana ai ance bak'on ka Annabin ka , haka toh na gode ,babu komai barin je kar hajiya ta nemeni, ta fice tana fita malika ta aje abincin kan table taci gaba da gyaran kayan ta,
Sai da ta gama duk abun da zatayi snn tayo alwala tayi sallar magrib snn taci abincin ta gama ta haye gado ta fara dailing numbar din ummi bugu d'aya ta d'aga, sunyi hira sosai sannan ta kashe tayi addu'a ta kashe light d'in d'akin ta fara bacci
[10/1/2017 Dija waziri□□: cikin bacci taji kamar ana kiran ta bud'e ido tayi taga ahlam tsaye a kanta zumb'ur ta mik'e tace ya akayi fuska a tamke tace ki tashi 6am tayi hajiya na neman ki kuma dokar gidann e duk wata yar aiki 6 nayi tagama bacci, wani mahaukacin kallo malika ta jifeta dashe toh fa ni ai lokacin da nazo hajiya bata sanar dani haka ba don haka banga wanda ya isa ya sani tashi 6 ba,to nidai na sauke hak'k'i idan yaran gidan suka miki wani rashin mutuncin babu ruwana, ta wuce ta fita murmushi malika tayi, rashin mutunci lallai ko zasu d'aukowa kansu dala ba gamma ai ni nafi k'arfin rashin mutunci don ni harda na saidawa ina dashi ,
amma zan musu uzuri na kwana biyu taja bargo ta koma baccin ta""

10:30

""Nabiha ce ta sauko daga sama tana k'walawa ahlam kira jiki na rawa ahlam tazo,na'am anty gani yawwa ina wannan yar aikin da aka kawo jiya Diyana take ko wa? Inda inda ahlam ta fara yi nabiha ce ta daka mata tsawa badake nake ba,au .....am .....tana d'aki tana bacci ,bacci kuma baki sanar da ita dokar gidan nan bane , kanta a k'asa tace na fad'a mata ,ok kin fad'a mata shine tayi kunnan shegu lallai yau zata gane kuren ta""

 ""kitchen ta shiga ta d'auko ruwa mai k'an kara tayi d'akin malika, tana shiga ta watsa mata a firgice ta mik'e tana fad'in subhanallah wani d'an kutumar uban ne ya zubamin ruwan sanyi a jiki.,yar masu gida ce ta zuba miki nabiha ta fad'a a tunzure ,kallon ta malika tayi kawai tayi murmushi a zuciyar ta tace yarinya baki san ko ni wacece ba amma muje zuwa ta mik'e ta shige toilet ,tabar nabiha gurin a tsaye kuma bata bata hak'uri ba,
mamaki abun ya ringa bawa ahlam a zuciyar ta tace lallai Diyana yar tasha ce ,rai a b'ace nabiha ta fita tare da cewa ahlam idan ta fito kice mum na kiran ta kuma ki kawo min tea d'aki ina jiran ki, toh kawai ahlam ke cewa""

""Malika ranta a b'ace ta fito daga wanka tasa kaya shigar daban daban tayi snn ta fita tayi part d'in mum, tana shiga ta tarar da su duka suna zaune suna kallo,
cikin ladabi ta russuna ta gaida hajiya da fara'a ta amsa tare da tmbyn me ya had'asu da nabiha, kallon hajiya malika tayi tace ina cikin bacci tazo ta zubamin ruwan sanyi batare dana san me ye laifina ba, kallon nabiha mum tayi tace Allah ka shiryamin ke nabiha mutum ya girma amma kullum jinki kike kamar kausar,
Diyana kiyi hak'uri kinji yanzu ki shiga d'akin dad d'insu ki gyara har falon shi yau zai dawo daga uk dan Allah kiyi aiki mai kyau mu zamu fita kinji idan kin gama saiki kulle ki kai key d'in d'aki na kinji ko, toh kawai tace snn ta tashi ta fita""

""Tana shiga d'akin ta fara binshi da kallo ta wani shu'umin murmushi Wanda bansan da wacce irin manufa take hakan ba, komai na d'akin white ne ,d'akin ya gaji da haduwa,fitowa tayi sad'af sad'af ta lek'a taga su mum sun bar falon da gudu ta fice ta koma part d'in su d'akin ta ta shiga ta dauko camera guda d'aya cikin wanda Abi dinta ya bata,sako shi tayi a hijab ta dawo part d'in ta shige d'akin,

tsofa camera'n tayi can wani lungu wanda babu wanda zai tab'a tsammanin akwai abu agun amma yana haska komai na d'akin da abun da mutun keyi,
Gyara ta soma yi sosai ta gyara d'akin tsaf,ta gama tasa turarukan wuta masu k'amshi snn taja kofar ta rufe,sitting room d'inshi ta shiga ta gyarashi shima sosai snn ta d'auko camera'n shima tasa inda baza'a gani ba ,1:20 daidai ta gama duk wani Abu da zatayi ta koma d'aki ta zauna don ita bata shiga harkan yan aikin gidan""

""Su asabe ko ita da sauran masu girkin gidan kam sai faman girke girke suke kala-kala,ahlam kuma sun fita da ita,
D'akinta ta shiga ta rufe da key ta d'auko system d'inta tana gyara setting d'in wani abu""

""K'arfe 4 su mum suka dawo suka samu an kammala komai d'aki mum ta shiga taga malika ta gyara mata shi tsaf ,murmushi tayi tace kai amma gsky Diyana ta iya aiki tafi duk sauran iyawa,kaya ta cire ta d'aura towel ta fad'a toilet ""

""Noor ce ta kalli ahlam tace idan kinje part d'inku kice dlDiyana tazo ina son ganinta , toh ahlam tace ta wuce ,
tana zuwa ta doshi d'akin malika murd'a kofar dakin tayi taji a kulle ,k'wank'wansawa ta soma yi ,da sauri malika ta rufe system d'in ta maida shi wadrobe tazo ta bud'e,
tana ganin ahlam ce ta had'e rai meye zaki kama bugawa mutane k'ofa, itama ahlam fuska a d'aure tace dama meye kuwa kinsan ai bazan buga miki k'ofa haka kawai ba toh aunty noor ce ke kiran ki,
Sakin baki malika tayi toh fa su aunty noor manya me zan mata ni fa bana son takura ehe don ko a gida babu wanda ya takurani,dariya ahlam tasa hhhhhh lallai ma ke d'innan gida fa kika ce nan ko aiki kika zo dole ki jure wulak'anci barin ma irin na yan gidan nan gara ma aunty noor akan aunty nabiha,
Kin gannin nan irin wahalar da nake sha gidan nan ko ba don wani abu ba da tuni nabar musu gidan su bana hutawa sai dare yayi,ke wani rashin mutuncin ma sai baban su ya dawo don shi baya k'aunar talaka ko kad'an,
murmushi kawai malika tayi ba tare da tace komai ba ta wuce,direct d'akin noor ta shiga tana shiga ta ganta jikin mirror tana shafa mai,
K'arasowa tayi ta d'aura hannun ta kan madubin tace noor gani , d'ago kai noor tayi tace me kika ce, k'ara maimaitawa malika tayi nace noor,
Ok toh,ke kuma naki salon kenan bakiji abun da yan aikin gidan nan ke cemin ba? naji kuma na sani amma ni bakina bazai iya fad'a ba,oh toh haka kika ce toh d'auki rigan can ki goge min yanzu ina so nasa,
kallon ta malika tayi tace bazan iya ba aeli lokacin da aka kawoni hajiya bata ce na dinga muku aiki ba,mik'ewa noor tayi ta fara nuna malika da yatsa wai ke me kike d'aukar kanki ne who do you think you are? da kike wa mutane raini kinga zafa ki iya barin gidan nan,
toh idan nabar gidan sai me ko kina tunanin ,sai kawai ta tuna wani abu tayi shiru,ina tunanin me k'arasa mana ,ke kinga get out of my room, ko da yake bama kisan me nake cewa ba don dake da jaki duk d'aya kuke a wurina,
malika ta cika har wani ja ta soma yi tsabar ranta ya b'aci kawai tayi shiru ne saboda ta tuna abun da ummi d'inta tace mata,kasa jurewa tayi tace ai kinsan idan anyi jaki to dole za'a samu jaka kinga kenan munyi anko ni jaki ke kuma jaka,ta bud'e k'ofar ta fice ranta a b'ace""

""Daskarewa noor tayi a wurin da mamakin wai yau ita mai aiki ke zagi kuma mai aikin ma ta gidan su lallai dole tabar gidan nan yau
A hasale ta fice tayi d'akin mum zaune ta sameta tana d'aura d'an kwali cikin kulawa ta juyo da kallon ta kan noor,noor meya sameki naga ranki a b'ace wani abun aka miki?
kuka ta saki😭 mum gsky ki kori Diyana wlh bata da mutunci ko kad'an dama tsiyar talaka kenan ya za'ayi tazo karkashin mu amma bamu da iko da ita,It's ok mamana sorry kema meye na shiga harkan Diyana,diyana iya aikin dad d'inku zata ringa yi ,ga ahlam ina ita na sama muku?
toh mum shikenan dan ahlam ita ce yar aikin mu bamu isa musa ita diyana ba? noor saurareni sosai diyana yar aikin dad d'inku ne ahlam takuce so bana son wani rigima kuma ki fita sha'anin diyana,kika san me ya kawota aiki ku dinga wa mutun uzuri mana kuma kullum ina muku nasiha akan wulak'anci bashi da kyau amma kun k'i ji,
haba ku kullum baku da magana sai k'yamar talaka wlh kubi duniya a hankali mahaifinku duk ya cusa muku d'abi'ar banza ku dai matane ,kuwa kanku fad'a""

""Horn d'in mota sukaji da gudu kausar da nabiha suka sauka don taran dad d'insu,motoci ne keta shigowa harabar gidan dukkan su iri d'aya wani guda d'ayane kalar shi daban a tsakiya ,sojoji naga sun fara fitowa cikin motocin snn daga bisani suka bud'e wa ogan su ya fito shima""

Ni dija sakin baki nayi ina kallon ss tafida ban taba zatan haka yake ba duk ina masa kallon wani kyakkyawa ne ashe abun ba haka bane

""Ss tafida bak'i ne yana da jiki ga k'aton ciki yanda kukaga tunbin shehu hassan kano da kiran haka yake"" 😂😂😂😂😂😂

""Da gudu su kausar sukayi hugging d'inshi idan kuka ganshi gangar yaran saiku rantse bashi ya haife suba saboda sun fishi kyau kuma su farare ne,
D'aukar kausar yayi yana kissing d'inta yaran suka mara masa baya suka shiga ciki tare da PA d'inshi""

sai naji comments dinku.....

Nice dai taku a kullum khadija waziri😍😍😍😍

Edited by Zee Yabour
□□□□□□□□□

FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dijawaziri

dedicated to all my fan's

©(OHW)

January 2017

Page

16&20

da fara'a hajiya ta k'araso tayi masa sanun da zuwa snn suka k'arasa cikin falon , suka zauna ,sun danyi hira kad'an da yaransa snn daga bisani ya wuce dakin shi don yad'an watsa ruwa, hajiya ma tabi bayan shi don had'a masa ruwan wanka.....

**** bai wani jima ba ya gama ya fito kaya marasa nauyi yasa sanan ya fito falo don cin abinci.....zama sukayi gaba d'ayan su kan daining suna cin abinci tunda alhaji ya shigo gidan.....duk yan aikin gidan suka dena zurga zurga dama dokar gidanne haka idan yana falo basa zuwa part din harsai ya shiga d'aki ko, ya fita.....

"""malika ce tsaye a farfajiyar gidan tana wasa da flaws din dake jere a wuri PA din alhaji ko na tsaye kusa da wata mota cen nesa da ita amma hankalin shi duk yana kanta.....

"""phone dinta ne taji ya fara ringin da sauri ta duba screen dind wayan , taga an rubuta Al zaro ido tayi waje□

Snn tayi wani ajiyar zuciya silent tasa wayan ta wuce da gudu ta shige d'akin ta , ta kulle .....

daukar wayan tayi.....nidai ban san da macece ko namiji take wayan ba jidai nayi tana cewa, eh dan allah aci gaba da aiki kar ayi wasa yau mai gidan ya dawo so a fara aiki yau don bana so mu wuce, 6month .....kashe wayar tayi ta fara dariya ga dukkan alamu dariyar mugunta take yi.....

gidan ambassador binta.....

gidane dan daidai mace d'aya shi ba babba sosai ba kuma shi ba k'arami ba, ita kad'aice a gidan sai yan aikin ta guda biyu baba hanne da nawwal

Ambassador binta kawar ss ta fida ce tun tana yar mata har zuwa yanzu, suna abota....

nawal ce ke goge tv taji k'aran bud'e kofa unty binta ta gani ta fito daga d'akin ta sanye da waya a kunnen ta, zama tayi kan kushin,sai da takai wurin 30minute suna waya kuma ba da kowa take ba ilah ss tafida, ji nayi tace ok alhaji ganinan zuwa gidan naka maganar bata waya bace.....

daki ta shiga ta dauko mayafi tace nawwal bar aikin nan muje mu dawo.....ajje towel din hannun ta tayi da sauri ta shiga d'aki ta dauko hijab dinta suka tafi.....

****basu dade ba sai gasu a gidan ss tafida falon bak'i suka shiga hajiya tazo suka gaisa ,sanan ss tafida shima yashigo tare da PA dinshi don duk inda zaije suna tare.....

ganin ta yayi tana kaiwa da kawowa cikin falon duk tayi zufa duk da sanyin ac dake tashi, zama yayi a razane don yasan duk yadda akayi akwai problem.....binta meke? faruwa nasan akwai matsala tunda na ganki haka,

"Hmmmmm.....idan kace matsala kafadi kadan matsaloli zaka ce , kar6i wanan ka karan ta kaga me aka rubuta.....

**cikin rashin fahimta ya kar6a ya fara karan tawa.....

sulaiman salisu tafida saurareni sosai kaji ba lalle ka gane ,me magana ba .....ina so ka zauna cikin shiri don nima yanzu zan fara aikina .....ke kuma munafuka fatima binta kema ki zauna cikin shiri don dake zan fara,

wlh !wlh!!wlh!!!
sai naga bayanku sai na rama butulcin da kukayi a rayuwa ss tafida kai butulu ne ,allah ya isa tsakanina dakai na barku lafiya sak'o daga mk

cire hular dake kanshi yayi ya maida kallon shi kan absd binta , waye kuma mk waye shi miye had'in mu dashi? meyake nufi damu? mai muka masa ?"

""" alhaji banida amsar tambayoyin ka nima dazan samu a bani da so nake..... kuma ni abun dake dauren kai shine ya akayi har ya shigo gidana ya ajje ba'a sani ba ,duk matakan tsaron dake gidan, tow allah ya kyauta kawai bara zana ce rabu dashi alhaji ya fad'a.....

shidai PA din alhaji yana jin duk abun da suke.....

****malika ko na dakin ta ta kulle tana kallon duk maganar da alhaji suke a system dinta.....
kashe system d'in tayi tare da tunanin wani abu.....

After one month letter

~ ss tafida ne ya fito daga falon bak'i tare da abokin shi suna hira.....

wato alhaji tafida wlh ni kaina zan so ace kai zakaci ba6enan don nasan zanfi kowa samu.....Hmmm alhaji shamsu kai dai bari munanan muna ta kanfen kai dai ka cigaba da tayamu, ae wato alhaji tafida inaji a jikina kai zakaci cox yanda kake kyautata ma talakawa , dole su so ka amma fa idan kahau ina tausayin su,

dariya suka sa gaba d'ayan su, kai alhaji shamsu baka da kyau fa, a'a dama ina zanyi kyau uban gidana bai koya min ba.....tow haka abun yake jirani barin shiga gida na dauko abu yanzu zan dawo, ok tow nikam ka samen a mota alhaji shamsu ya fad'a yana yar dari irin tasu ta yan duniya.....

After 2 minutes

cikin sauri ss tafida ya fito daga shikin gida wurin da alhaji shamsu yayi parking ya nufa.....bud'e kofar yayi ya shiga ya sameshi ya junguna da jikin kofar mortar kamar yana bacce.....

**** kallon shi ss tafida yayi yana shamsu kai kuma miye haka daga barinje na dawo kuma sai ka b'ingire da bacci..... shiru yaga yayi bai ce dashi komai ba, mamaki abun ya bashi ya ta6a shi yaji baya motsi kuma baya numfashi , jawo hannu shi yayi da sauri ya saki yana kiran sunan allah , abun daya gani ya balain rikitashi.....

ganin shi yayi hannun shi duk jini cikin shi kuma an caka masa wuk'a , fita yayi a motar da gudu yana kururuwa yana kiran sojojin gidan ,

dagudu sukayi yuya suka zo suna tmbyn lfy , nuni yayi musu da motar da gudu suka nufi gurin suma abun yayi masifar basu tsoro da mamaki comishina of police suka kira cikin gaggawa sukayi mass bayanin abun dake faruwa,

mota biyu sukayi cikin gagawa suka nufi gidan *ss tafida* basu jima sosai ba suka isa..... bincike suka farayi cikin gidan....

INTERMISTON

1 hours letter

ss tafida ne zaune a falon sa shida su hajiya , sai zufa yake had'awa ,

daya daga cikin police din da aka turo ne ya shigo falon yana shiga alhaji ya mik'e..... ya ake ciki kun gane waye ya aikata ?"

murmushi police d'in yayi yanda yaga alhaji lokaci daya ya rud'e akan abun da baya masa wuya, zama yayi kan kujera ,alhaji a gsky lamarin ga ya daure min kai bama niba mutani dayawa .....

ace duk irin matakan tsaron dake cikin gidanan a rasa wanda yaga wanda yayi kisa gsky abun da had'in baki.....munyi iya bincike mun kasa gano waye yayi wanan aika aika, sai dai kawai wata pepar da muka tsinta jikin wuk'ar da akayi kisar da ita, kaga abun da aka rubuta.....

***jiki na rawa ya kar6a ya fara dubawa kamar haka.....

somun ta6i kenan wanan shine kadan daga cikin aiki na , bara zana ta farko by mk

shiru yayi ya fara tunanin ina ya ta6ajin suna mk.....sai da yayi dogon tunani sanan ya tuno letter din da binta ta kawo masa wata daya daya wuce.....

police dinne ya katse mai tunanin da yake.....am alhaji muna so kad'an mana bayani akan mk dinan duk yadda akayi shi ya aikata ko sanshi?"

gyaran murya alhaji yayi snn ya k'ara da cewa " a gsky ban san ko shi waye ba kuma ban san me yake nufi dani ba .....tow babbar magana tow a gsky alhaji za'a samu problems cox wanan abun zai iya sa jama'a suki sa6ar ka , kuma ni a ganina a cikin gidan ka makashin yake cox wanda yasan sirrin ka shine kawai zai iya haka.....

tow ni waye zai aikata min haka babu wanda yasa sirrina sai PA dina suhai kuma bana tunanin zaici amanata, don yana da amana kuma mun dade dashi ,

sai dai ko a cikin sojojin dake min tsaro.....ok alhaji ni zanyi handling caus dinka zan fad'ada bincike insha allah zan gano waye wanan , ni zan tafi by the way my name is abdul zan kiraka idan na koma office sai kayi seving ya bashi hannu suka gaisa..... ya tafi.....

"""wato alhaji nima abun yaban mamaki ace wai duk irin tsaron da 'ake a gidanan ace an shigo anyi kisa , cewar hajiya ,

tow nima dai abun ya d'auren kai daga barin shiga na fito kawai fa.....

tow Allah shi kyauta aniyarsu ta bisu tunda babu abin da muka masu.....acewar hajiya tana shirin tashi,

malika kam na la6e jikin kofa tana jin duk abun da suke , ganin hajiya tayo wajen ne yasata fita da gudu.....

sai naji commets dinku.....

dan allah idan kunga badai daiba ku gyara min.....

Nice dai taku a kullum mai kaunar ku khadija waziri😍😍😍😍
□□□□□□□□□

FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dijawaziri

dedicated to all my fan's

©(OHW)

2017

Page

21&26

part din hajiya ta shige da mugun gudu dama an sata gyaran d'akin ss tafida, ji tayi tayi karo da mutun , da sauri ta dago don ganin waye"" noor ta gani fuska a daure.....matsawa tayi baya tana yihakuri dan allah wlh ban san kina wurin ba ,

tow dama yaushe zaki san ina wurin tunda dama ke dabbace mara hankali, kazama , kallon noor malika tayi rai a bace ,ke noor kibar ganina cikin gidanku zaki nemi ki rainamin hankali, dakinsan ni wace da bakiyi gagawan fad'amin abun da kika fad'a ba .....kinsan meya kawoni aiki gidan ku?"

tow wlh ki iya bakin ki don ni ba irin yan aikin ku bace dazaku kalla ku take babu abin daya maku zafi.....

""dariya noor ta kyalkyale dashi😂 nasan meya kawoki aiki mana.....miye dama zai kawoki daya wuce bak'ar talaucin dake adabarki keda iyayen ki, dama tsiyar talaka kenan keba kowaba kiringa nuna gadara da isa a gidan mutani, tow wlh mu bazaki mana ba.....

ran malika yayi matuk'ar 6aci da zancen noor , a hasale tace , ae shi talaka da kike gani bashi yaso ganin kanshi haka ba allah ne yaso, ya ganshi haka ,kuma haka zalika mai kudi.....

kinga ko allah yana iya kwace abunsa aduk sanda yaso kuma a lokacin daya so ya bawa wanda yaga dama, tow ko kinga muda muke talakawa bamu cire rai.....kum abu na k'arshe dazan sanar dake shine, kibi duniya a sanun ke macece kuma baki san wa zaki aura ba.....taja tsaki ta shige d'akin alhaji tabar ta wurin a tsaye.....

****

ran malika a 6ace ta gama gyaran dakin ta wanke toilet tayi morfing ta fito ..... rike da towel din datayi goge goge.....

tafiya ta somayi zata koma part dinsu.....ji tayi an kira sunan ta da tsawa diyana!!

tsayawa tayi kem ba tare data waiga ba .....

kara sowa nabiha tayi tasha gaban ta .....jeki gyaramin daki ahlam batanan mum ta aike ta kuma bacci nake ji, kiyi sauri.....

kallon ta malika tayi sama da k'asa sanan tace bazan gyara ba sai dai yau ki kwana a tsaye, inde ni diyana ce zan gyara miki d'aki.....

kut waike me kike daukar kanki ne dubeki fa yar talakawa dake , kinga aiki kika zoyi kuma dole kiyi nabiha ta fad'a.....

murmushin yake malika tayi ah bakiyi k'aryaba nabiha, aiki nazo amma bawa irin kuba wainda baku san darajan mutun ba, don wlh danamuku aiki gara namutu cikin talauci.....aikin banza ina arziki kuke tak'ama dashi ko tow kuje duniya ce ta ishi ku riga da wando , aikine dai bazan ta6a .muku ba har nabar gidanan saboda , ba zaman ku nake ba.....

kinga ma tafiyata don tsayawa cacan baki dake ba girmana bane taja tsaki ta fice.....

tana fita nabiha ta haye sama tana kuka, dakin mum ta shiga ta samu , mum nawa noor fad'a

fad'awa tayi jikin mum din tana kuku , cikin kulawa maman ta fara tmbyn meya sameta..... nan ta kwashe lbrn yanda sukayi da malika ta fad'a.....

kai wai ku yaranan meke damun kune ?" yanzu haka fad'an da nake wa noor kenan tafita harkan diyana amma tak'iji , tow ku sani nifa bazan kori diyana ba don ta iya aiki idan kuma kuka sake tabar gidanan tow wlh kunji na rantse bazan sake kawo yar aiki ba, kuma duk zan kori yan aikin ku kucigaba dayi kuji ko dadad'i.....

kuma ku tashi kubar min daki tunda bakujin magana hajiya ta fad'a a hasale.....

mikewa sukayi jiki a sukwane suka fita, dakin su suka nufa, suna shiga nabiha ta fad'a kan bed tana kuka..... ita ko noor rosting char ta jawo ta zauna tana wasa da yatsar hannun ta,, ta fuskanci inda nabiha ke kwance.....

nabiha ! noor takira sunan ta d'ago idon ta tayi da sukayi jazur , ta sauke kan yar uwar tata.....na'am sis...

"kinga gara mu fita harkan diyana, tunda naga kamar ta lashe zuciyar mum , kinga wlh mum zata iya aikata abun data furta , kuma idan ta koresu ina zamu iya aikin gidanan..... wlh sis noor bazan yarda yar aiki ta ringa mana abun dataga dama ba wlh bari dad ya dawo saina gaya masa,

"tow nidai bazan fad'aba zanyi hakuri amma next tasake yimin wlh zan dauki mataki da kaina, noor ta fadi rai a bace

""nabiha ce tace ae wlh yau sai tasan wata zaga bari dad ya dawo.....

Tow yanzu dai it's ok , muje mu sami mum mu bata hakuri, kinga ranta ya baci noor ta fadi tana shirin tashi.....

nabiha ce tace ni babu inda zani ba ita tace mubar mata d'aki ba tow bazan sake shiga d'akin ba tunda ta tsanemu bata son mu.....

"kai nabiha mai yayi zafi haka karfa ki manta uwar kice.....

tow shi kenan dan uwatace sai ta ringa fifita wata banza akan mu ae wlh yau duk, abun da akemin sai na gayawa dad.....

"nidai ba ruwana kinga ma tafiya ta.....

next day

"dad ne ke kwalawa mum kira daga falo , da sauri tabar abun da take tazo falo , ta sameshi da shida kausar da nabiha zaune, na'am dadyn kausar kayi hakuri kana kirana ban zo da wuri ba na shiga toilet ne.....

"fuskar shi a daure yace me nabiha tayi miki?" Kinbi kin samu yara a gaba akan yan aiki , talakawan banza da hofi me za'ayi da talaka dama ae bauta shine daidai da su.....

haba dadyn kausar ya zaka ringa biyewa yaran ka.....cewar mum .....a'a dakata nifa duk neman danake akan yarana nake yi so bana son abun da zai 6ata musu rai.....

"ran mum a 6ace ta kalli su nabiha..... Kutashi ku bani wuri ana magana kun saka kuni kuna ji, tashi sukayi suka fita , maida kallon ta tayi kan dad pls alhaji idan zaka min fad'a ka dena min a gaban yara na.....

"tow nima ki dena 6atama yarana rai akan yan aikin ki idan kuma suka sake kawo min k'ara zan kori wanda tayi musu.....

kallon shi tayi da mamaki tace tow kayi hakuri dadyn kausar , murmushi yayi ok tow na hakura.....ina so ki tura wata daga yan aikin suje gest house dina a gyara min.....

tam bara nasa diyana da ahlam suje.....

Kiran su mum tayi ta sanar dasu.....wani shiumin murmushi malika ta saki dama abun da take so kenan.....

"dakin ta ta shiga ta dauko wata jaka da teday a ciki tasa hijab ta fita da shi.....drive ne yakai su tun karfe sha daya suka tafi basu suka gama aiki ba sai karfe biyu na rana.....fitowa sukayi zasu koma ahlam tace diyana kinbar tedy dinki kan tv fa.....kai barshi kawai na kausar ne idan sunzo ta dauki abun ta ..... nagaji bazan iya komawa ciki ba.....sunzo daidai kofar fita suka hadu da su ss tafida suna shirin shiga.....

"matsawa gefe sukayi suka, basu wuri sai da suka gama shigowa, malika ko sai satan kallon shi take dama bata ta6a ganin shiba tunda tazo gidan.....sai da suka gama shiga snn su kuma suka fita.....

~~~ cikin palon suka shiga suka zauna suna tataunawa akan batun siyasa, phone d'inshi ne yayi ringing, da sauri ya da'aga jinayi yace ,ok bara na turo PA dina yazo ya same ka , sai ya kashe.....
~~~

wani soja ya kalla a kusa dashi yace yaje ya kira masa PA dinshi a waje, haka ko akayi fita yayi da niyar kiran shi dai dai lokacin shi kuma prob isa ya dano motar shi da zumar shiga gidan.....

duba shi sojan yayi bai ganshi ba.....juyawa yayi don ya koma ciki ya sanar da alhaji bai ganshi ba, shigar shi keda wuya.....sukaji karan harbi harbe .....zunbar suka mik'e gaba dayan su zasu fita suga ko lfy, d'aya daga cikin abokan sane ya tsaida shi akan kar ya fita su kuma suka fice.....

suna fita suka taradda prob isa kwance cikin jini yana nishi sama sama.....cikin gagawa suka dau keshi zuwa hospital su kuma sojojin suka bi wanda yayi harbin da gudu , amma basuyi sa'ar kamashi ba.....

dai dai ana cikin tashin hankalin ne sai ga PA ya shigo yana nishi kamar wanda yayi wani aikin wahala.....kallon shi alhaji yayi cikin 6acin rai yace kai kuma miye haka ?" wlh alhaji nadawo daga wurin cin abinci ne sai naga sojojin gidanan suna bin wani shine na taya su.....ok yanzu kun kama shi cikin fargaba alhaji yayi maganar.....

girgiza kai PA din yayi alamar a'a.....had'a hanayen shi wuri daya alhaji yayi yace "shet yana wata irin nishi , tow wai ni waye wanan ne duk yanda akayi bibiyata yake so yake yaga bayana.....PA dinne ya katseshi da cewa amma lhaji kamar ba namiji bane kamar mace ne nidai a yanda naga gudun.....

"kai anya macece kuwa kamar fa namiji ne mace bazata iya ba.....

wayar shi ya ciro daga aljihu yayi dailing number police ya sanar dashi abun da ake ciki.....

mai gadi ne ya dauko ruwa zai wanke gurin jinin prob isa yazo zai zuba ruwa a gurin kawai yaga wata peper anyi rubutu da jan bairo.....

dauka yayi da har zai yasar tunda ba karatu ya iya ba sai kuma ya fasa.....ya mik'awa su alhaji takardan da sauri ss tafida yasa hannu ya karba ya fara karan tawa.....

ss tafida idan ina raye ban mutu ba sai naga bayan ka wlh sai na kashe ka, kuma wlh bazan ta6a bari kaci za6e ba don samun irin ku a matsayin shigabani hatsari ne babba.....wanan kad'an ka fara gani daga aikin mk

gumi ne ya fara keto mai bai san sanda ya cire hular dake kansa ba komawa ciki yayi ranshi a 6ace tare da tunanin waye wanan keta bibiyar rayuwar sa

~5:20 P. M~

Ss tafida ya dawo daga gest hours ya tarad da mummy zaune kan sofa tana karanta jarida kausar na gefen ta tana shan apple,

kara sowa yayi ya zauna .....kallon shi ajiya tayi tace alhaji yana ganka haka kamar kana cikin damuwa?" Ko wani abu ne ya faru?.....

"girgiza kai ya fara yi yana sharara gumi kamar ba ac a falon, wlh mummy kausar kisa akayi yau a gest house dina.....zaro ido hajiya tayi waje tare da fad'in subhanalah wa kuma aka kashe alhaji?"

Wlh prob isa aka harba dazu alhaji kasim ya kira yake sanar dani ya mutu.....inalilahi wa inna ilaihi rajiun kai jama'a tow allah yaji kanshi da rahama, amma wai waye yake maka wanan aika aikan ne haka?"

Hmmmm.....wako zai min daya wuce mak'iya na alhaji ya fad'a yana shirin cire babar rigar dake jikin shi .....tow allah shi kyauta cewar mum

2 week lettar

Alhaji ne zaune cikin d'akin shi yana duba wasu mihimar takar dunsa..... wayar shine ta fara ringin duba wayan yayi yaga an rubuta alhaji rufai,

zaro ido yayi waje yace tow me kuma zan yiwa president ya fara tmbyn kanshi.....daukar watan yayi daga 6angare nalhaji rufa'i ne yace ,

"hello alhaji tafida.....

"hello alhaji rufa'i afternoon ya aiki.....

"Alhamdulila komai lfy dama so nake gobe mu hadu a "hiltol akwai meeting da nake so muyi.....

"Ok Allah ya kaimu darai da lfy ya kashe wayar.....

"malika kuwa na zaune d'aki tana kallon duk abun da ss tafida keyi a laptop dinta.....tashi tayi ta bud'e wardrob dinta , ta dauko wani dan k'aramin box ta dawo ta zauna..... rufe system din tayi ta ajje shi a gefe.....

bude box din tayi ta dauko wani d'an karamin takalma na yara ta fara shafawa tana hawaye.....ta fara tunano abun daya dade yana damun zuciyar ta .....

sis i love u kin zame min komai a rayuwa ta.....me two my littel sister ta fad'i tana shafa gashin ta, kwance suke kan tanga memen gadon su suna bacci kanwar ta mik'e a razane tana ihu.....mikewa yayar tayi da sauri sis ya akayi meya sameki? cikin kulawa take tmbyn ta.....share hawayen da ke zuba a idon ta tayi tare da cewa.....

"sis nayi mafarki wai kin gudu kin barni murmushi yayar tayi haba my sis yaza ayi na tafi na barki duk son , da nake miki , ki kwantar da hankalin ki ina tare dake har tsahon rayuwa ta kinji.....

kuka malika ta fashe dashi tana sis l love u i really love u.....

kuka take shasheka sosai kamar ranta zai fita haka tayi tayi har , bacci 6arawo ya sace ta.....

WASHE GARI

Yau ya kama monday ss tafida ne ya fito a gagauce cikin shirin zuwa offece, zai fita hajiya ce ta tsaida shi da ewa.....

alhaji ina zakaje haka kake wanan uban sauri ko karyawa bakayi ba?"

mummyn kausar na makara da yawa kina gani har 9:30 tayi kuma ina da meeting da president ne gashi 9 daidai mukayi za'a hadu, bari kawai idan naje cen nanemi wani abun naci.....

"" fita yayi cikin sauri ya nufi wurin motar sa kiran Benz ya bude gidan baya ya shiga.....drive yaja suka tafi PA dinshi kuma da sauran sojoji sukabi bayan sa a wata mota daban..

basu tsaya ko ina ba sai babban hotel din dake garin abuja wato heltol.....

kuyi hakuri da wanan ba yawa.....

Ina mika godiyata ga dunbin masoyana kai harma da makiyana nagode da soyyar da kuke nunamin😍?□□□□□□□□□

FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dijawaziri

dedicated to all my fan's

©(OHW)

2017

Page

21&26

part din hajiya ta shige da mugun gudu dama an sata gyaran d'akin ss tafida, ji tayi tayi karo da mutun , da sauri ta dago don ganin waye"" noor ta gani fuska a daure.....matsawa tayi baya tana yihakuri dan allah wlh ban san kina wurin ba ,

tow dama yaushe zaki san ina wurin tunda dama ke dabbace mara hankali, kazama , kallon noor malika tayi rai a bace ,ke noor kibar ganina cikin gidanku zaki nemi ki rainamin hankali, dakinsan ni wace da bakiyi gagawan fad'amin abun da kika fad'a ba .....kinsan meya kawoni aiki gidan ku?"

tow wlh ki iya bakin ki don ni ba irin yan aikin ku bace dazaku kalla ku take babu abin daya maku zafi.....

""dariya noor ta kyalkyale dashi😂 nasan meya kawoki aiki mana.....miye dama zai kawoki daya wuce bak'ar talaucin dake adabarki keda iyayen ki, dama tsiyar talaka kenan keba kowaba kiringa nuna gadara da isa a gidan mutani, tow wlh mu bazaki mana ba.....

ran malika yayi matuk'ar 6aci da zancen noor , a hasale tace , ae shi talaka da kike gani bashi yaso ganin kanshi haka ba allah ne yaso, ya ganshi haka ,kuma haka zalika mai kudi.....

kinga ko allah yana iya kwace abunsa aduk sanda yaso kuma a lokacin daya so ya bawa wanda yaga dama, tow ko kinga muda muke talakawa bamu cire rai.....kum abu na k'arshe dazan sanar dake shine, kibi duniya a sanun ke macece kuma baki san wa zaki aura ba.....taja tsaki ta shige d'akin alhaji tabar ta wurin a tsaye.....

****

ran malika a 6ace ta gama gyaran dakin ta wanke toilet tayi morfing ta fito ..... rike da towel din datayi goge goge.....

tafiya ta somayi zata koma part dinsu.....ji tayi an kira sunan ta da tsawa diyana!!

tsayawa tayi kem ba tare data waiga ba .....

kara sowa nabiha tayi tasha gaban ta .....jeki gyaramin daki ahlam batanan mum ta aike ta kuma bacci nake ji, kiyi sauri.....

kallon ta malika tayi sama da k'asa sanan tace bazan gyara ba sai dai yau ki kwana a tsaye, inde ni diyana ce zan gyara miki d'aki.....

kut waike me kike daukar kanki ne dubeki fa yar talakawa dake , kinga aiki kika zoyi kuma dole kiyi nabiha ta fad'a.....

murmushin yake malika tayi ah bakiyi k'aryaba nabiha, aiki nazo amma bawa irin kuba wainda baku san darajan mutun ba, don wlh danamuku aiki gara namutu cikin talauci.....aikin banza ina arziki kuke tak'ama dashi ko tow kuje duniya ce ta ishi ku riga da wando , aikine dai bazan ta6a .muku ba har nabar gidanan saboda , ba zaman ku nake ba.....

kinga ma tafiyata don tsayawa cacan baki dake ba girmana bane taja tsaki ta fice.....

tana fita nabiha ta haye sama tana kuka, dakin mum ta shiga ta samu , mum nawa noor fad'a

fad'awa tayi jikin mum din tana kuku , cikin kulawa maman ta fara tmbyn meya sameta..... nan ta kwashe lbrn yanda sukayi da malika ta fad'a.....

kai wai ku yaranan meke damun kune ?" yanzu haka fad'an da nake wa noor kenan tafita harkan diyana amma tak'iji , tow ku sani nifa bazan kori diyana ba don ta iya aiki idan kuma kuka sake tabar gidanan tow wlh kunji na rantse bazan sake kawo yar aiki ba, kuma duk zan kori yan aikin ku kucigaba dayi kuji ko dadad'i.....

kuma ku tashi kubar min daki tunda bakujin magana hajiya ta fad'a a hasale.....

mikewa sukayi jiki a sukwane suka fita, dakin su suka nufa, suna shiga nabiha ta fad'a kan bed tana kuka..... ita ko noor rosting char ta jawo ta zauna tana wasa da yatsar hannun ta,, ta fuskanci inda nabiha ke kwance.....

nabiha ! noor takira sunan ta d'ago idon ta tayi da sukayi jazur , ta sauke kan yar uwar tata.....na'am sis...

"kinga gara mu fita harkan diyana, tunda naga kamar ta lashe zuciyar mum , kinga wlh mum zata iya aikata abun data furta , kuma idan ta koresu ina zamu iya aikin gidanan..... wlh sis noor bazan yarda yar aiki ta ringa mana abun dataga dama ba wlh bari dad ya dawo saina gaya masa,

"tow nidai bazan fad'aba zanyi hakuri amma next tasake yimin wlh zan dauki mataki da kaina, noor ta fadi rai a bace

""nabiha ce tace ae wlh yau sai tasan wata zaga bari dad ya dawo.....

Tow yanzu dai it's ok , muje mu sami mum mu bata hakuri, kinga ranta ya baci noor ta fadi tana shirin tashi.....

nabiha ce tace ni babu inda zani ba ita tace mubar mata d'aki ba tow bazan sake shiga d'akin ba tunda ta tsanemu bata son mu.....

"kai nabiha mai yayi zafi haka karfa ki manta uwar kice.....

tow shi kenan dan uwatace sai ta ringa fifita wata banza akan mu ae wlh yau duk, abun da akemin sai na gayawa dad.....

"nidai ba ruwana kinga ma tafiya ta.....

next day

"dad ne ke kwalawa mum kira daga falo , da sauri tabar abun da take tazo falo , ta sameshi da shida kausar da nabiha zaune, na'am dadyn kausar kayi hakuri kana kirana ban zo da wuri ba na shiga toilet ne.....

"fuskar shi a daure yace me nabiha tayi miki?" Kinbi kin samu yara a gaba akan yan aiki , talakawan banza da hofi me za'ayi da talaka dama ae bauta shine daidai da su.....

haba dadyn kausar ya zaka ringa biyewa yaran ka.....cewar mum .....a'a dakata nifa duk neman danake akan yarana nake yi so bana son abun da zai 6ata musu rai.....

"ran mum a 6ace ta kalli su nabiha..... Kutashi ku bani wuri ana magana kun saka kuni kuna ji, tashi sukayi suka fita , maida kallon ta tayi kan dad pls alhaji idan zaka min fad'a ka dena min a gaban yara na.....

gyaran murya Minal tayi ta kalli Malika tace tow Malama Malika dake zamu fara, murmushi Malika tayi tace tam, ina jin ki ,yawwa ko zamu iya sanin dan takaitacen lbrn ki ?? Dasauri Malika ta dago manya-manyan, idonta masu haske ta kalli Minal

tace "no cox" Babana ya sani kuma nayi alkawarin babu mai kuma sanin labarina sai munje kotu , ok tam babu damuwa tunda shugaban mu ya sani, Minal ta fada tana murmushi , malika bincike ya nuna cewa kece kika cakawa Alhaji tafida wuk'a da, hannun ki don sheda ya nuna a jikin wukar da akayi aika aikan da ita kuma an rubuta cewa kin cenja suna lokacin da kikaje aikin gidan Alhaji Tafida munaso muji hujjarki nayi hakan da kuma amsa laifinki da bakinki??

"Yes nacenza suna a gidan S.s Tafidane sakamakon kur a ganeni kuma ina da hujjan yin haka ,caka wuk'a, kuma da ake zargin ninayi Babu banuna a ciki kuskuren daya da nayi shine ta6a wukar yayin dana samesa cikin halin da yake....

Tow munji amsar ki amma taya zamu iya sanin bake ce kikayi yin kurin kashe Alhaji ta fida ba, waye shedar ki??

Allah shine shedana sai kuma Ahlam da muka shiga tare da ita, cewar Malika ,Minal ce tace tow mun gamsu da batunki Malika zamu kara bincike sosai wurin gano ko hannun waye yayi kokarin kashe ss fida , bari mu dawo gareki ta nuna nawwal duk sun masu tambayoyi sosai kuma sun amsa , su Minal sundan jima da tafiya sannan su judge mukyar suka iso.....

sunyi bincike sosai jurge muktar ya kar6i komai shi zaiyi shara'a

Hajiya Rabi ce zaune kan gado a hotel din da suka sauka tayi kicin kicin da fuska jamar me neman yin fada, jurge muktar kuma yana zaune kan wani madai-daicin carpet dake shinfide a tsakar dakin ,sanye da glass a idon shi yana duba wasu takardu, matsowa tayi kusa dashi ta fuskan ceshi sosai.....

Alhaji ! jurge muktar yaji kiran Hajiya Rabi amma bai ko kulataba bare ya dago ya kalleta ya cigaba da duba takardun gaban sa ,a fusace tace haba Alhaji magana fa zan maka kuma kamin banza.....

Dagowa yayi ya cire glass din idon shi ya kalleta kinga rabi idan maganar Malika zakimin bana son ji don nariga na gama magana, bazanyi abun da Allah zai kamani ba ni duk abun da zanyi a rayuwata gaskiya nake bi , iya adalcin da zanyi nariga nayi bazan yarda na fitar da malika daga gidan ajiya ba har sai munyi bincike mun gano gaskiya, nasan, Malika bata aikata Abun da ake zargin ta dashiba ,ki fahimceni bawai bana son Malika bane yasa nayi haka Ina bin adalcine da abun daya dace shiyasa kikaga nabarta gidan ajiya.....

tow Alhaji ae gani nayi ba laifi bane don ka yi belin ta idan yaso sai murika shiga kotu ba tare da ance tana gidan ajiya ba, tunda naga mutani dayawa nayin hakan.....

Hmmm Rabi kenan bazaki gane meyasa nayi haka ba sai nan gaba ,kuma da kikace mutane nayin haka ae rashin tsoran Allah ne, da kuma cinhanci da rashawa, da yayi yawa a kasarmu shi yasa bazamu ta6a cigaba, ba 'a rayuwa ni muktar nayi Alkawarin har na koma ga Allah bazan ta6a kar6an cin hanci ba kuma duk abun da zanyi zanyi shine a gaskiya da 'amana bazan ta6a tauye ma talaka hakin saba wlh yau ko d'anda na haifa a cikina ,ne yayi ba daidaiba kuma aka shiga kotu dole na yanke masa hukunci daidai da yanda zan yankema kowa ,kuma koda shugaban kasane yayi ba daidaiba shima dole na yanke masa hukunci daidai da lefin sa saidai kuma a kasheni daga baya....

kai amma Alhaji kasa duk jikina yayi sanyi ,lalle Alhaji yau na kara yarda cewa abin duniya bai dameka ba da za'a ringa samun irinka a kasarnan da talaka bazaiyi

kukaba kai bama takala kawai ba da kowama bazai kukaba lalle Alhaji da ace zaka zama shugaban kasarnan tamu da anga cenji da yawa hajiya Rabi ta fada..

murmushi kawai Jurge muktar yayi ya maida glass din shi ya cigaba da duba takardun sa.....

Hajiya rabi ta jima tana zaune a wurin tana kallon mijinta, kawai tana murmushi tare da godema Allah daya bama miji mai adalci da tausayi da sanin ya kamata, bata san sanda ta furta Allah ka barmu tare mijina da murmushi ya dago ya kalleta yace ameen matata, itama murmushin tayi tace Alhaji ka tashi kaje ka kwanta haka pls dare fa yayi....

Rabi ina naga ta bacci d'iyata na gidan ajiya ko kin manta gobe nizanyi shari'a a kotu ne aini banga ta bacci ba yanzu ma haka brrt Abbas nake jira akwai wasu copy din takardu dazai kawo min....

Tow Alhaji Allah ya taimaka yakuma bamu nasara ,way ya batun S. s Tafidan har yanzu bai tashi ba??

Ameen rabi ,wlh har yanzu dazu mukayi waya da doctor din yace min bai tashiba amma yana tunanin zuwa gobe koda dare ko jibi zai iya tashi...

Tow ubangiji Allah yasa ya tashi kodon musan waye ya kashe matarsa dakuma shi da akayi yinkurin aikawa lahira....Ameen Rabi ae ni banaso S. s Tafida yayi mutuwar shahada nafiso ya wulakanta a duniya

Tow Alhaji Allah dai yayi mana maikyau don nima hakan nafi so S. s Tafida shine silar rugujewar farin cikinmu a rayuwa shena ya bata mana duk wani buri a rayuwar mu hakika mutuwarshi hutune ga Alumah...

Wannan haka yake rabi .....

WASHE GARI

Yaune za'a shiga kotu.....
□□□□□□□□□

FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dijawaziri

wannan shafin nakine sajna(mrs abdul)Allah ya barmun ke ya bar zumunci ina alfahary dake sister love you❤😘

©(P.W.F)

Page

65&66

Saturday morning
Ayau ne za'a daura auren alhaji tafida da hajiya binta...

12:02pm

babban masalacin dake garin abuja cike yake makil da jama'a kowa sai farin ciki yake ss tafida ko baki yaki rufuwa manyan mutane sun halara sosai shugaban kasa ne kawai bai jeba a manya-manyan mutani saka makon rashin jituwar da basayi da alhaji tafida, 12:30 na bugawa aka daura auren ss tafida da hajiya binta wai zokuga murna wurin su kamar bai ta6a aure ba....

nan danan labari ya cika gari har a bbc sai da aka nuna bikin,
Judge muktar na zaune a tangamemen falon sa wanda ya gaji da haduwa ya tankwashe kafa yana shan drink yana kallon bikin ss tafida da hajiya binta wani shiumin murmushi yayi tare da maganar zuci wanda baisai ya fito fili ba Allah buwayi gagara misali, duniya budurwan wawa yau zaka amsa duk wani laifi daka aikata a kotu....

bayan daurin aure kowa ya watse, ss tafida ma ya dawo gida wurin karfe 4:00 PA dinshi yazo ya sameshi, a falo suka gaisa, am dama alhaji so nake na je gida amma ba jimawa zanyi ba zan dawo.....tow ina fatan dai lfy? "ae ba komai kamayi kokari daka jima bakaje kaga iyalan kaba yanzu yaushe zaka tafi? yau da anjima tunda ba nisa ne da garin namu ba tow allah ya kaimu idan ka gama shiryawa sai kazo ka samen.....tow alhaji ya tashi ya fice, bai jima da fita ba wani soja ya shigo rik'eda farin pepar a hannun shi da salama.....

ss tafida na ganin shi da fada yace waiku ban hanaku shigo min wuri bane ? "im sorry sir" sako aka bada kuma babu kowa dazai kawo banga PA dinka ba kuma, shiyasa nazo da kaina.....tow kar ka sake min haka idan babu wanda zai kawo min ka barshi idan na fito sai kaban, ok sir ya mika masa ya fice....

komawa yayi kan kujera ya zauna ya fara bude wa yana karan tawa.....what lalle ma wannan jugde muktar din wai me yake nufi ne tow allah ya kaimu monday din zanga dani dashi wazai yi wining.....tsaki yaja ya tashi ya shige daki yana haki.....

yana shigewa malika ta shigo falon ashe duk taji abun da yake fada, takardan ta dauka ta bude ta karan ta wani shiumin murmushi ta saki wanda ya kara fito da asalin kyawun ta....

Nabiha da noor kam sun gama hada kayan su tsaf jira kawai suke ranar tafiyan su yazo...zaune suke a falo suna kallo wurin karfe takwas na dare"ss tafida ya shigo ya samesu rabon da ya zauna yaji damuwar su har ya manta bare yasan halin da suke

ciki....ina mai baku hakuri yarana kwana biyu ban samu zama bane shi yasa bamu zauna munyi magana dakuba , noor me kike son fadamin tun tuni?"

wlh ni harna manta ma abun da nake son fada maka dad , tow yayi kyau ina fatan kunyi murna da sabuwar uwar dana sake maku?

dariyan "yake sukayi suka kalli juna suka hada baki yes sosai ma dad happy marriage, muna tayaka murna da sake aure, tnx yarana ina sonku ,muma muna sonka dad.....

hawaye noor ta fara yi tare da cewa dad idan namaka ba daidai ba ka yafemani bana so na mutu da hakkin kowa a kaina.....

Subhanallah me yasa kike man irin wannan zancen noor bafa nason zance mutuwa.....

dad ko kana so ko bakaso dole mu mutu dole mu koma ga allah shiya sa ake so a kullum mutun idan yazo bacci yayi tunanin abubuwan daya aikata ya nemi gafaran allah sabi da bai san ranar komawa rageshi ba nabiha ta fada tana kuka....

Kinyi gsky kanwata ya allah ka tsarkake mana sucuyoyin mu allah ka rabamu da sharrin azalumai allah kamin sakayya da azalumi alagun gumin mutumin daya rabani da badurci na da ace zan ganshi yanzu wlh babu abin da zai hananin fansar budurcina masu hali irin nashi ubangiji ka shirya su noor ta fadi tana kuka.....

Jikin ss tafida gaba daya mutuwa yayi dayaji irin kalaman da yaran sa suke fadi girgiza kai yayi kawai a zuciyar shi yace da kunsan waye uban ku da kunyi nadama.....

noor nabiha kuyi haku duk kan tsanani yana tare da sauki me kuka nema kuka rasa a rayuwa da har zaku ringa tunanin mutuwa dukiya allah ya baku jin dadi allah ya baku me kuma kuke nema?

Aljanna muke nema dad duk abubuwan daka lisafa babu abin da zasu mana duk a duniya zamu barsu tow miye amfanin su cewar noor.....

Hmmm Allah kawa mum albarka ashe sammu take lokacin da take nuna mana gsky mu kuma muna ganin kamar ta tsanemu ne,cewar nabiha....

ran ss tafida yayi masifar 6aci dajin kalamen nabiha.....oh wato ni bana baku kenan ko?" Ku tashi kuban wuri shashashe kawai ku yarane har yanzu baku san me duniyar take ciki ba kuma tunda kuka ce haka zakuga cenji daga gareni yaja tsaki mtsssss" da kuka duk suka tashi suka bar masa falon

A 6angaren hajiya binta kam sai shirye shire take na komawa gidan ss tafida gobe duk ta salami yan aikin gidan ta banda nawwal ita kadai ce zata tafi da ita....

zaune nawwal take cikin dakin ta duk abun duniya ya dameta ta rasa ta inda zata iya daukan carset din ,sai sak'awa take tana kwance wa, wata shawara ce tazo mata ta tashi da sauri tayi dakin hajiya binta da salama.....

zaune ta samesu ita da k'awayen ta suna hira ta rusuna ta gaida su, fuska a yatsine suka amsa da lfy ke kuma wace?"

Kin jiki da wata tmby salamatu sai kace baki san wace nawwal ba me aiki na?" Cewar hajiya binta

Oh dama ita ce ae gani nayi ta dad'a girma , tow ya bazata girmaba ke din dama haka kike? nawwal meya faru?"

kanta a kasa tace Aunty dama so nake na ce maki zan je gida yanzu babana ya kirani yake sanar dani mamata ba lfy, Allah sarki tow zaki dawo ko kuma idan kin tafi kin tafi kenan?

Eh zan dawo data samu sauki, tow Allah ya kiyaye ga wannan kiyi kudin mota ta mik'a mata 5k, hannun biyu tasa ta kar6a tayi godiya ta fice.

tana fita tayi dakin ta ta dauki wayan ta ta kira baban ta bugu daya ya daga...

Hello nawwal ya kike?

lfy qlau baba yau zan dawo gida,

Meyasa zaki dawo nawwal bacin baki dauki abun daya kawo ki cikin gidan ba?

baba na kasa dauka kuma gashi yanzu gobe zata bar gidan da na bari ne idan ta tafi a daren washe garin naje na dauka ba tare da kowa yasan nashiga gidan ba,

tow hakan ma yayi Allah ya kaimu,

Ameen baba sai anjima...

A 6angaren malika ma ta gama hada kayan ta tsaf jira kawai take jibi tayi taje ta dauki ragowan takardun da zata dauka ta gudu don sun gama magana da Al zasu hadu gidan ss tafida sai sushiga dakin tare.....

washe gari tun karfe 4:00 motocin daukar amarya sukazo kawayen amarya duk sun gama shiri amarya kadai ake jira ta fito su tafi bata jima ba kuwa ta fito suka shiga mota suka dauki hanyar maitama.....

A gidan ss tafida kam su hajiya adama sai aiki suke abinci kala kala malika ma dakin ss tafida ta shiga ta gyare shi tas , aka saka turaren wuta gidan ya dume da kamshin tura ruka....

noor da ahlam ko ranar ko fitowa basuyi ba bare susan me ake ciki

A bangaren hajiya khadija kow dataji lbrn auren ss tafida da hajiya binta sai da taji babu dadi duk da bason ss tafida a ranta kuma aranar ne ta tabatar cewa hajiya binta bata da alkawari .....

an kawo amarya gidan ta yan kai amarya har sun gama abun da zasuyi wurin karfe bakwai kowa ya watse ya rage saura hajiya binta da yaran ss tafida dako fitowa su gaida ta basuyi ba.....

By khadija
[2/21, 01:01] Dija_waziri□□: [2/20, 00:12] Dija_waziri□□: □□□□□□□□□

FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dijawaziri

* wannan shafin nakune yan group dina dija novel ina alfahari daku□*

ina mai Baku hakuri da rashin jina 2days dan Allah wainda suka min magana akan naturo musu novel duk wanda yaga ban tura masaba yayi hakuri wlh abubuwa ne suka min yawa ina fatan zaku min uzuri😊

©(P.W.F)

Page

67&68

Wurin 8 o'clock dai-dai s's tafida ya shigo fallo ya tadda su noor sunyi jugum-jugum kamar wadan da aka wa mutuwa....

Karsa shiga yayi da salama ,a tare suka amsa da "wa'alaikumus'sallam" sannun da dawowa dad... Yace yawwa sannuku, ya naganku haka kamar bakwa farin ciki da zuwan sabon uwar danayi maku?...

murmushin yake nabiha tayi babu komai dad, kawai dai muna kewar aunty fatama ne, yanzu muka rakata mota, wai gobe zata tafi kaduna ita da yara, shine muka dawo muka zauna..... Oh tow ae yayi kyau, kunje ko gurin auntyn taku?..

"A'a bamu jeba tukun, dama yanzu muke shiri n zuwa sai gaka... Okay tow kuje ni barin je dakina na huta....

kallon noor yayi dake faman danna waya, don tunda ya fara magana bata tanka masa ba, bare ta ce wani abu, ke bazaki tashi ki bita kuje ku samu auntyn taku ba ne?... ya fada yana washe baki kamar gonar auduga.....

d'agowa tayi ta kalleshi fuska a yamutse, tace zan tashi, barin dauko wani abu a daki sai nazo naje, Nabiha jeki ina zuwa.... A'a kije ki dauko muje tare kawai ina jiran ki,..

Murmush s.s tafida yayi kawai ya shige daki don yau jinshi yake kamar wanda bai ta6a aure ba sai akan hajiya rabi...

kinga Nabiha idan zaki ga hanya, don nikam babu inda zani, ae bayau na ta6a ganin taba, so kingama ni tafiyata daki don bacci nake ji, cewar noor...

Nabiha ma yamutsa fuska tayi, tace tow sis in banda abunki dama kina tunani zanje ne, matar da taci amanar uwata, ta rabata da jin dadin ta, wlh ko ita wacece, bazan sata a sawun uwa ba, bare har kallon mutunci ya hadani da ita....

Noor tace, idan ma munzauna gidan kenan ko?.. Ae daga gobe shike nan munyi bankwana da wannan gidan, zamuje mu nemi mummy duk inda take...

suna cikin haka, sai ga Ahlam dauke da flaks din ruwan zafi, da cup, da kayan tea, ta shigo falon, ta nufi kofar dakin hajiya rabi....

Nabiha ce ta daka mata tsawa, keee!!! ina zaki kai wainnan..? da rawan jiki Ahlam tace, dakin hajiya zan kai,... tow dama kece mai kawowa ko kuma aikin kine?... Ina Diyana ae naga aikin tane kow?...

Baba Adama tayi tayi da ita akan ta kawo tace wai ita tabar aiki don gobe zata bar nan gidan babu wanda ya isa yasata aiki tayi, shine baba Adaman tace na kawo.....

Tsaki sukaja gaba daya suka shige daki, suna shiga Nabiha tace sis wlh banso diyana ta tafi gobe ba, don ita ce daidai da wannan yar iskar matar dad din.....

Hmmm ke nabiha bazaki gane bane, amma ni na fuskanci wani abu game da Diyana wlh akwai abun da take nema wurin dad, kuma ba yar aikin gaskiya bace, Noor ta fada tana shirin cire kayan jikinta....

Zaro ido Nabiha tayi waje,😳 ban gane ba sis, kina nufin kice duk abun da take plan ne???..

HMMM kinga sis abar zancen kawai, ni wankama zan shiga...
Nabiha ma shashan tar da zancen tayi, ta nufi kan gado ta kwanta tana dannan wayarta....

A bangaren ss tafida ko har yayi wanka ya shirya cikin riga da wanado, na bacci yana zaune kan royal bed dinshi yana danna laptop....
Ya kai kusan minti 30 kafun ya fito, yayi dakin hajiya rabi dauke da fara'a a fuskar shi.....

WASHEGARI

ya kama monday misalin karfe 10 na safe, zaune suke kan daining suna cin abinci , Nabiha da Noor sai kallon mahaifin su, suke don yau sun tashi sunji wani son sa ya kara shiga zuciyar su wanda har suna tunanin anya zasu iya aikata abun da suke da niyya yau.....

hajiya rabice tayi gyaran murya, tare da cewa Noor Nabiha yana ganku haka kamar an muku wani abu? "tana kallon su

murmushi nabiha tayi tace babu komai aunty kawai dai yau dinne kwata kwata garin baya mun dadi ji nake kamar akwai abun da zai faru da wani nawa yau.....

murmushi s.s tafida yayi, tare da cewa, kai Nabiha ki dena irin wannan tunanin haba ae nikam babu abin da zai faru damu ke dama zuriyata gaba daya don wlh mutun yayi kadan yaci galaba akaina.....a'a dad kur kace haka, nabiha ta fadi ni yar kace, dole idan kayi ba daidai ba na gyara maka hakan ba laifi bane dad I'm sorry to se gaskiya akwai abubuwan da kake da dama wanda mu a matsayin yaran ka bamu jin dadin hakan, dad yakamata aduk abun da zakayi a duniya ka ringa cewa insha allah, kuma ka ringa tuna mutuwa aduk abun da zaka aikata, hakan yana kara ma mutun imani

duk abun da suke noor bata sani ba don ta lula duniyar tunani...

Buga tebur din da suke s.s tafida yayi da karfi ke!!!
Nabiha, buga tebur dinne ya dawo da noor daga duniyar tunanin data fada a razane, nifa na haifeki bake kika haifen ba da zaki kalleni kice zaki min wa'azi tow ki iya bakinki na fada maki ko kin fini sanin abun da nake ne shashasha kawai....

Alhaji hakuri zakayi ae yarinya ce dole sai ka ringa mata uzuri hajiya binta ta fada...

Noor ce tace dad kayi hakuri, tana kuka dan Allah Nabiha bawai ta fada maka wannan maganar don ta 6ata maka rai bane amma tunda hakan bai maka dadi ba tow kayi hakuri zata ringa kiyayewa nidai ina rokon ka da ka yafe min ta hada hannun ta biyu tana kuka....

Tuni jikin s.s tafida yayi sanyi da yaji magan ganun noor duk sai yaji ya fara nadamar furucin da yawa nabiha yaji soyyar yaran ta kara shiga zuciyar shi ,dakewa yayi ya cigaba da fadan shi....

kunga nifa ba mutunin banza bane kuma zan dauki mataki akan ku wawaye kawai ya mike ya bar falon cike da bakin ciki hajiya binta ma tashi tayi tabi mijin ta.....
kallon _kallo nabiha da noor suka fara yi , kara fashewa nabiha tayi da kuka tace sis wlh na gaji , nagaji da halin dad bazan iya ba.....

tow nabiha ya zakiyi uban kine babu yanda kika iya dashi , kuma idan kinyi, hakuri anjima kadan ma, bazaki kuma ganin saba , zamu bar masa gida.....

A bangaren su Malika kam, zaune duk yan aikin gidan suke , suna cin abinci a kitchen, malika ce ta fito dauke da jakar kayan ta , Ahlam ce ta fara ganin ta diyana ina kuma zaki ?.....suka hada baki gaba dayan su suka tambya.....

murmushi tayi tace zan kai kayana, gidan abokiyar tafiyata ne, wadda muka zo tare da ita, anjima kadan zamu tafi so da nakai zan dawo.....

Baba , Adama ce tace tow Diyana sai kin dawo, ga kudin aikin ki noor taban dazu tace na baki, kunce zanin ta tayi tana kokarin fito da ,kudin malika tace, a'a Baba ki barshi kawai na baku kudin bana buk'atar su..... .

Sakin baki sukayi suna kallon ta baki buk'atar su fa kika ce???.....

yes haka nace kow nayi laifi ne?.....

A'a bakiyi ba amma abun da mamaki, baba, adama ta fada ki gama wahalar kuma sannan kice baki son kudin.....

Murmushi tayi tace kur ki damu , baba adama ,ae sakai ne barin je na dawo kur dare yayi.....

bayan fitar Malika baifi da yan mintina ba Ahlam ,ma ta fito sanye da, mayafi a kanta ,batare da kowa ya ganta ba, ta fice.....

Malika ko tana fita ta nifi tasha , takai kayan ta ajiya sannan ta nemi me mota ta sanar dashi karfe 4:50 na Asuba yazo ya dauketa a maita tayi masa kwatan ce nan sukayi ciniki ta kama hanya.....

tana cikin tafiya taji wayan ta ya fara ruru da sauri ta duba taga AL ce ba shiri ta daga daga bangaren Al ta fara magana....

Hlo sis kina ina ne inaso mu hadu yanzu yanzu.....

Ok gani a tasha, yanzu da zan koma gida, amma ina jiran ki kizo ki samen....

Tow jirani ganinan zuwa....

basu jina da gama wayar ba sai gata' ta iso.....

Cikin sauri suka nemi wani wuri suka ke6e, Malika wai ya muke ciki ne? kinsan fa yau za'ayita ta kare me kike ganin yaka mata muwa s.s tafida?.....tow nima tunanin da nake kenan kin ganni bani da tsoro zuciyata a bushe take kawai so nake na cikawa abun alkawarin sa shi yasa na fasa zancen kisan amma da wlh babu abin da zai hanani kashe s.s tafida da hanuna don na huce kadan daga cikin takaicin da nake ji....

tow malika tunda kince banda kisa ya zamuyi don nima nayi tunani sosai akan kisan da mukace zamuyi naga ba daidai bane a matsayin mu na musulmai kuma masu hankali.....

haka ne AL ni shawara ta shine kawai mu dauki abun daya kaimu ae baza'a barshi haka ba akwai ranar kin dillanci kuma damun koma abun zai afkashi a babban kotun musulunci, kinga ko ae dole a k'wata mana hakkin mu.....

Kin kawo shawara mai kyau Malika hakan ma zamuyi Allah ya mana jagora, wurin karfe nawa zamu shiga dakin nashi?.....

Wurin 11 daidai koya kika gani.....

Ae ni abunda kika ce Malika shi zanyi yayi sosai.....

Malika ce tace tow nikam zan koma gida Al akwai abun da zanyi kinga yanzu har 4;30 tayi.....

tow sis sai anjiman kow....

Nan sukayi salama kowa ya kama gaban sa.....

KADUNA

Hajiya ce zaune kan sofa sai rarashin Nasreen take wadda sai kuka take akan a kawo ta wurin dad, dinta.....Nasreen yanzu kin fiso ki rabu dani ki koma wurin dad ,dinki??.....a'a mum so nake yau na ganshi don nayi mafarki dashi wai ya mutu.....

murmushi hajiya tayi tace kai kema dai nasreen har yanzu kina yarinta keda kika cemin na dena kiranki da beby kin girma kuma shine kike abun yara....

Ta6a baki nasreen tayi tace mum menayi?.....murmushi hajiya tayi tace kin manta cewa mafarki karya ne ba gaskiya ba tow ki kwantar da hankalin ki dad dinki lafiyan shi kalau , tow mum na hakura, yawwa gud gil mai jin maganar maman ta
□□□□□□□□□

FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dijawaziri

i dedicated this page to u my sweetheart jannat thanks you for everything my lovely sis i love you so much, Allah ya barmu tare ya kuma Kara zumunci□□□

godiya gareku masoya na nagode da kulawar ku da kuma kwarin guiwar da kuke bani, muniba ina k'aunar ki kamar yadda kike k'auna ta Allah yabar zumunci😘😍

©(P.W.F)

Page

69&70

Wurin karfe takwas da arbain, Malika ce zaune kan kujera a Kitchen, tana cin abinci tana bin wakar dake tashi a wayan ta, baba Adama ce ta shigo tana mata magana ,amma sam bata kula taba don hankalin ta nakan wakar datake ji.....

Diyana tunanin me kike tun dazu nake maki magana amma kamar badake nake ba?..... Oh wlh ban jikiba Baba, tow damun yaushe zaki jini kin kasa kunne kina jin wakar da ko gane abun da ake cewa bakiyi ,wai inama kika samo waya maikyau haka da tsada don ban ta6a ganin ki dashi ba?.....

Hmmmm Baba kenan wlh kinban dariya, wayace maki banjin abunda ake fadi?? Kow don kinganni haka kina nufin banda ilimi ne?.....

A'a niban ceba, ae ganinayi mu acen k'auye ,bamu cika barin yaran mu suyi karatun boko ba.....

Hakane Baba kinyi gaskiya ,amma nikam nayi karatu don ko su noor bazasu nunamin ilimi ba kadara ce tasa har kika ganni nazo nan gidan aiki,da kuma cikar wani buri..... waya kuma da kike tambayan inda na samo ,dama tuncen da abina nazo ,kawai dai ganin tane baku ta6ayi ba.....

Baba Adama ce tace tow ke kuma meya faru dake haka da kike son cika buri kuma waya miki wani abu???.....

Baba kibar zancen kawai bazan iya fada maki ba.....tow diyana Allah ya fitar dake kuma Allah ya saka maki idan ma wani abun aka maki, Ameen Baba nagode da Adu'ar ki a gareni Allah ya saka maki.....Ameen diyana nice zan maki godiya bake ba kin fasa tafiya yau dinne?....

Eh tow wata k'ila zan tafi wata k'ila kuma sai gobe da Asuba don bazan bari gari ya waye ba, Amma aken samuna ,ma nafison ,natafi yau.....

tow Allah ya kaimu ae kamar yau ne idan kin bari sai goben, ni a ganina kawai ki bari sai gobe , sabo da yanzu dare yayi.....tow Baba zan gani .....

****

Tow masu karatu bari mu lek'a muga halin da Fahad ke ciki

Kwance yake cikin wani karamin daki, mai dauke da wendor daya, kofar dakin ba wani babba bane sosai, kanshi a nade shi da bandeg.....

Wasu gara den maza ne guda biyu,suka bud'e kofar dakin da mukulli suka shiga, Fahad na ganin su yayi saurin tashi daga kwanciyar da yake, Bayin Allah, dan Allah ku sake ni na tafi, wlh na gaji da zama cikin wannan dan karamin dakin ,wai mai nayi maku ne?? d'aya daga cikin garaden mazan, ne yayi magana ,baka mana komai ba Fahad, kuma mu bamu , muka dauko, ka muka kawo ka nanba Ogan mune ,kuma ka shirya yanzu zamu tafi dakai zuwa gidan da yake....

Cikin sauri Fahad ya shirya suka fita duk sai yaga garin ya cenza masa don rabon shi da fitowa tun randa yabar gidan s.s tafida , mota yashiga suka tafi....

wani katafaren gida suka shiga zubi da tsarin gidan yayi,gidan bawani babba , bane sosai , fitow sukayi duka, suka zagaye shi daya kuma ya rike shi don dak'ar yake iya tafiya ji yake kamar zai fadi, wani katon falo suka shiga suka zauna sanyi a.c ne kawai ke tashi da kamshin turaren wuta masu dadi, wani katon mutun suka gani ya fito daga wani daki, yana ganin su yace har kun iso?? kufa dama nake da niyan kira

don Oga yariga da ya fita don yana da abun yi, yanzu sai kujira shi zuwa gobe da safe, ga d'aki cen ku sashi ciki ya nuna masu dakin.....hakan ko sukayi.....

karfe shabuyi da minti daya nadare...

gidan shiru kowa ya kwanta.....Malika da A.l ne suka fito sanye da hijabi akan su ,suka nufi part din su s.s tafida, dai dai sun zo bude kofar shiga cikin falon sukaji motsi kamar ana bin su, juyawa sukayi suka fara ,dubawa amma basuga kowa ba, A hankali suka bod'e kofar suka shiga falon, wuta, a kashe suka samu hasken wayan su suka kunnan suka fara haskawa har suka kai kofar dakin s.s tafida.....

ihu suka somaji cikin dakin na tashi a hankali, bada karfi sosai ba, kallon A.l Malika tayi anya burin mu zai cika kuwa?.....kamar fa baiyi bacci ba.....ke kiyi a hankali kur ajimu mana amma ihun miye yake tashi haka cikin daki? A.l ta,tambaya a razane.....Ohhhho ina zan sani Malika ta bata amsa.....

A.L ce tace tow yanzu taya za'ayi mu shiga sis???.....

kinga A.l nifa zuciyata tariga ta bushe kawai mushiga komai ta fanjama fancen, tana fada ta fara kokarin bude kofar.....riko hannun ta A.L tayi A'a malika kar kiyi sauri bud'a wa, cikin 6acin rai Malika ta kalleta dallah sakeni haba matsoraciya kawai idan bazaki iyaba tow nikam zanyi ,Malika bata jira amsar Al ba ta shige dakin.....

Innarilahi wainna ilaihi rajiun, shine abun da malika ta furta yayin data ga halin da s.s tafida yake ciki

kubiyo ni zuwa gobe zakuji komai☺
[2/23, 01:32] Dija_waziri□□: □□□□□□□□□

FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dijawaziri

*Wannan shafin nakune yan PERFECT WRITERS FOUROM kuna burgeni wurin hadin kanku uban giji Allah yabar zumunci ya kara hada kawunan mu ina Alfahari daku □□□

©(P.W.F)

Page

71&72
Innarilahi wainna ilaihi rajiun

Shine abun da Malika ta furta, yayin dataga halin da S.S tafida yake ciki'.....

Salatin da Malika, tayi shi yayi saurin shigo da A.L cikin dakin, meke farywa Malika naga kina salati? Dabaya A.L ta koma yayi da itama taga S.S Tafida. Auzubillah! hasbunallah!! waya masa haka sistar??.....

Ko kula A.L Malika batayi ba, da sauri tayi kan S.S tafida tana kokarin zare wuk'ar dake soke a cikin shi, shiko sai birgima yake yana kakarin mutuwa jini sai fita yake ta bakin sa....Ji'jigashi Malika ta soma yi tana fadik, karka mutu baka sanar dani inda kasa takardun company din kaba, ka fada min inda kasa shi....Juyawa idon shi suka somayi nan danan ya sankare, wani wawan ihu ,Malika ta saki wanda har sai dayasa A.L furgita.....

Dagudu A.L tayo kan malika wadda ta burkice ta dawo kamar mahaukaciya , sis tashi mu fita kur azo a ganmu ayi tunanin mumuka kashe shi....Malika na rike da wukar A hannun ta ,tana shirin ajiyewa kawai sukaji an banko kofar dakin da "mugun karfi'....

A furgice! suka maida kallon su kan kofar Noor da Nabiha suka gani cikin shiri kamar wainda zasu bar gida...Nashiga uku!!
Wayyo Allah!! sun kashe dady, Nabiha ta fada tana shirin karasawa kusa da gadon S.S tafida....

Noor ma ihu tasa tare da nuna Malika da yatsa , yanzu cin amanar da zaku mana kenan?? Sakayyar da kuka mana kenan?.....Hardake Ahlam? keda nake gani mai hankali'.....

Walahi bamu san komai akan kisan Alhaji ba Noor wlh babu sa hannun ko daya daga cikin mu Alham ta fada tana kuka.....Dallah yiwa mutani shiru, munafukan, banza da hofi ,kawai Ae wlh iyayen ku sunyi asaran haihuwa, banzaye jakuna , kuma Wlh! Wlh!! Wlh!!! Kotu ce kad'ai zata rabamu daku Cewar Noor.....

Cikin zafin nama Malika ta kalli Noor ta fara nunata da yatsa,ke ki iya bakin ki, kin fahimta kow?" yau zan sanar daku koni wace ko nace muku komu suwaye ke inbanda abunki, ki fad'amun tun ranar da nazo aiki nan gidan kinga nayi kama da masu aiki?.....

Ke Noor duk zancen da zakuyi yanzu bashi zai ficce muba, kije ki kira sojojin gidannan ki sanar dasu halin da ake ciki ,kuma ki taso aunty binta ki sanar da ita azo akai dad hospital ko Allah zaisa yana da sauran nufashi, a duniya Nabiha ta fada tana kuka.....

Hakan ko akayi da gudu Noor ta fita waje taje ta kira sojojin cikin sauri da tashin hankali sukayi yuya saka shigo cikin gidan, dakin ss tafida suka nufa ita kuma tayi dakin Hajiya binta da godu don ta sanar da ita abun dake faruwa cikin daren.....

Tundaga bakin kofar dakin tayi saranda ihutasaki wanda yayi sanadiyyar fitowan sojojin dake dakin S. S Tafida da gudu abun data gani yayi masifar bata tsoro ,a sume suka zo suka sameta wasu suka fara kokarin dagata wasu kuma sukayi dakin da gudu.....

Abun da suka gani suma yayi matuk'ar basu tsoro da mamaki Hajiya Binta suka gani kwance cikin jini bakinta sai fitar da wani farin kunfa me yauki yake sai wata yarinya tsugune kusa da ita Dago ido tayi ta kalle su jikin ta sai rawa yake.....

Sanda yarinyar ta dago saida birona ya fadi tsabar mamakin wacece na gani nawwal ce....

Cikin gaggawa aka daukesu duka zuwa asibiti harda Noor data suma.....

Ba'afi minti talatin da fitar dasu S.s Tafida a gidan ba ,saiga police mota biyu suka shigo gidan, sunyi bincike sosai kafun nan suka tatara su malika da alham, da nawwal, tare da yan aikin gidan duka akayi dasu policetetoin.....
[2/24, 20:08] Dija_waziri□□: Nabiha sai kaiwa da kawowa take a kofar d'akunan da aka kwantar da su Noor, babu abin dake fitowa daga bakinta, sai Allah yasa, kursu mutu su barta.... Tana cikin haka sai ga wasu nurse ,sun fito, cikin Sauri Nabiha taje inda suke, sister lfy ina fatan babu wanda ya mutu??.....Cikin tausayawa d'aya daga cikin nurse din ta kallin Nabiha ta dafa kafad'ar ta, "i'm sorry kanwata(sister) "Allah yayi ma mahaifiyar ku cikawa, "what " innarilahi wainna ilaihi rajium ya ilahi, tow dad, da Noor fa??

Alhaji tafida yana motsi yanzu haka manyan likitoci ne akan shi don ganin sunceto rayuwar sa 'amma gsky shima gani nake kanar zaiyi wuya ya rayu.... Ita kuma dayar yarinyan an samata ruwa har yanzu bata tashiba dogon suma tayi, yanzu munaso ki kira manya don suzow, su tafi da gawan marigayiyar kur abarta, ta jima... ...

Kuka sosai Noor keyi kamar ranta zai fita suko nurse din sai bata hakuri suke abun tausayi....

Nikaina dija taban tausayi sosai😭

WASHE GARI

Magana duk ta baza gari babu garin da basuji mutuwar Ambassador binta ba da kuma S.S tafida....

KADUNA

judge muktar ne zaune yana karanta jaridar daly trust, kamar Wanda aka tsikara ya kunna t.v yana kunnawa yakai tashar labarai, ya cigaba da karatun jaridan sa...

Hajiya Rabi ce ta nufo falon rike da glass cup da shayi a ciki shigar ta keda wuya kafun ta zauna idon ta yakai da kallon T.V abun tada gani ya razana ta ba shiri ta sake ruwan shayin dake hannun ta k'asa, faduwar cup dinne yayi sanadiyyar d'agowar judge Muktar daga karatun jaridan da yake, da sauri yayo kanta lafiya? rabi meya faru ??....Nuna masa T.v ta somayi ba shiri shima ya kallah, hoton malika ,da Ahlam ,da Nawwal ya gani, tow mekuma malika tayi? naga ana nunata a T.V??

Zama sukayi gaba dayan su , don sauraron abun da za'a fadi game dasu

Labari da dumi dumin sa ,Ajiya ne aka kama wainnan yan mata gida uku da kukagani dumu dumu da laifin yinkurin kashe babban dan siyasar a kasarnan wato *Alhaji Sulaiman Salisu Tafida*, Misalin karfe shaburi na Daren jiya ,wanda tare da matarsa wanda itakan tariga ta amsa kiran Allah *Ambassador binta*.... Hukuma sun nemi da yaran su amsa laifin su amma sunki fir ga abun da yaran suka ce....

Ni sunana amalika muktar, wadda akafi sani da ,diyana ,maganar kisan S.S Tafida da ake zargin mu'muka ,kashehi ba gsky bane don muma haka muka zo muka ganshi kuma sanda naganshi cikin halin da yake nayi matukar farin ciki da hakan ,saboda barin irinsu a duniya ba karamin hatsari bane..

tow Malama Malika miye hujjan ki na fadin haka?? Ina da hujjoji, da yawa, amma bazan fadesu ,yanzuba sai munje gaban alk'ali....

Tow Malama Malika ko zamu iya sanin waye babanki a kasar nan?

Sunan babana *judge muktar*, "what "judge muktar dana sani? Kina nufin kicemin ke yar sace??

Kwarai da gaske niyar sace ko baka yarda bane? Eh ban yarda ba sai naga zahiri...

Tow masu kallon mu kunga hiran da mukayi da, d'aya daga cikin yaran da sukayi aika aika a gidan ,Alhaji tafida ,wadda take ikirarin ita yar babban Alkali mai zaman kansa, ne wato Judge muktar, tun a safiyar yau, yan sanda suka mik'a case, din ga babban kotun tarayya dake garin abuja

Innarilahi wainna ilaihi rajiun, yanzu malika Abun da tajawo min kenan? judge muktar ya fada....Alhaji kur kayi saurin yarda wlh jikina ya bani ba malika ce ta kashe S.S Tafida ba ka yarda da magana ta.....

Taya zan yarda da maganarki rabi bacin ga zahiri kina gani, Alhaji kenan nidai nasan malika bazatayi haka ba, tow rabi nima bangama yarda ba, bamuci ta zama ba ki tashi ki shirya, mutafi abuja ni zan yi shara'a ,barin kira barrister Abbas na sanar dashi ,yaje ya samu su malika kafun mu isow.....Tow Alhaji barin yi sauri na shirya....

A 6angaren hajiya khadija kow har ta isa garin abuja tun da taji zancen hadda Noor a gadon asibiti,

Zaune suke Noor har ta farfad'o daga dogan suman da tayi sai kuka suke mum na basu hakuri, kuyi hakuri Ae bai riga ya mutu ba insha Allah zai tashi, ba kuka zakuyi masa ba ,Adu'a zaku masa, mummy diyana ta cucemu wlh bazamu yarda ba ,duk da, dad bai mutuba sai munga bayan su cewar Nabiha.....

Hmmm Nabiha Diyana bata cuceku ba mahaifinku shine ya cuceku , hausawa sunyi gsky da sukace ranadubu ta 6arawo rana daya ta mai kaya , duk yadda Akayi akwai abun da baban ku ya musu shiyasa suka je daukar *FANSA* ku zuba ido idan anje kotu zakuji kamai kuma kucigaba da hakuri.....

Cikin zafun rai Noor tace tow mum koma meya musu bai kamata ace sunyi yin kurin kashe shiba kuma duk bakin su daya har yar aikin aunty rabi.....ke Noor bakisan dalilin dayasa suka masa haka ba ki bari zamuji dalilin su....

Kuma yau barin fada maku Abin da baku sani ba, nima sai yau nasan dashi Fahad shine yayan Diyana "what bamu gane ba mum?? su Noor suka hada baki suka tmby

"Yes"yadda kukaji na fada mahaifiyar fahad kawatace sosai Diyana kuma ba sunanta kenan na gsky ba sunan ta Malika "is a long story bazan iya baku lbr yanzu ba.....

Malika da Ahlam da Nawwal ne zaune abayan kanta😆 Malika sai satar kallon Nawwal take wadda duk a tsorace take

gawannan kuyi hakuri dashi abubuwa ne suma nin yawa sai gobe insha Allah zancigaba
□□□□□□□□□
FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dija_waziri

Wannan shafin nakune masoyan buk din fans a 'Allah ya bar so da k'awna ya bar zumunci #1 luv😍😘❤

(P. W. F)

page

75&76

Rana bata karya .Yau ne ranar da za'a fara case din Hajiya Binta da S. S Tafida. Kotu ya cika sosai da jama'a, abin ku da Abun daya shafi manyan yan tsiyasar kasa, Hajiya khadija da Noor da Nabiha da Fadil sa sauran yan uwansu duk sun hallara, tare da shedun su. Haka ta bangaran Su malika ma su Hajiya Rabi Su Ladi duk sun halara suma.....

Yansandane suka shigo dasu Mulika ,cikin kotun duk kansu an daure masu hannu Hajiya Rabi na ganin malika taji wani zafafan hawaye sun kwaranyi mata, da sauri ta kauda kanta daga kallon su Malika tayi saurin goge kwalar daga idon ta, nan aka tsaidasu gefen da aka tanadar musu ,Ahlam da Nawwal sai wiki- wiki suke da ido duk sun tsorata da irin kallon da mutani ke jifarsu dashi...ita kuwa Malika sunkuyar da kanta tayi tana mezubda hawayen bak'in ciki

kotun yayi shiru lawyas duk sunzo babu abin dake tashi cikin kotun sai nagan ganun su da suke ,kasa -kasa

Karfe tara na cika kuliya ya shigo ,tini kowa ya mike tsaye ,sai daya zauna sannan jama'a suma suka zauna.Nan mai karanto kara wato maga takarda ya karanto , barrt sunusi lawyan wanda yake kara kenan ya fara tashi ya gabatar da kansa da kuma mataimakin sa wato barrt safiya, tashi tayi tad'an rusuna tace my lord snn ta koma ta zauna. bayan duk sun zauna sai barrister Abbas ya tashi ya gabatar da kan shi. tare da mataimakiyar shi wato barristar Minal ta tashi tayi dan rusuna gami da cewa my lord bayan haka ne Aka fara aiwatar da shar'ah

Barrt Sunusi ne ya fara fitowa gaban mai shari'ah , cikin shiga irin tasu ta barristers, rike da biro bic a hannun shi.....

Kara dan rusubawa yayi a gaban Alkali sannan ya fara fado hakkin Hajiya Rabi da S.s Tafida Abun da su Malika sukayi musu A matsayin su na mutane ,

Bayan haka barrt Sunusi ya nemi izinin fara gabatar da shedun sa.ya farane da kiran Baba Adama, mai aikin gidan S.S tafida.Baba Adama ta fito.bayan tayi rantsuwa ta ,tabbatarwa kotu zata fadi komai ba face gaskiya. Ya fara tambayar ta wacce ita a gidan S.S Tafida, kuma meta sani game da wainda Ake tuhuma da laifi?. gyaran murya tayi tace ni yar aikin gidan ce shekara da shekaru muna tare dasu duk ina gidan Aka haifi yaran gidan ,Bansan komai Akan wainda Ake tuhuma da laifi ba haka zalika ban ma ta6a tsamanin Diyana da Ahlam sunsan junaba sai randa abun ya faru Abu daya dazan iya fada shine dama idan muna zaune Diyana takan ce mana akwai burin da take so ta cika data cikashi zata koma gida.haka dai barrt Sunusu yaci gaba da mata tambayoyi, har izuwa ranar da abun ya faru wanda Baba Adama ta tabbatarwa kotu cewa ranar diyana ta hada kayanta akan zata koma gida wanda daga baya tace ta fasa sai washe gari.ta kuma shaidawa kotu cewa a wannan daren ranar talata da misalin karfe goma na dare sunyi hira sosai dasu malika kafun kowa yaje ya kwanta wannan kenan . bayan barrister Sunusi ya koma ya zauna ne barrt Abbas shima ya ma Baba Adama tambayoyi.Bayan haka Barrt sanunsi ya nemi fitowar Noor gaban kuliya ,a tsorace ta fito ,ko da barrt sunusi ya fara mata tambayoyi game da Wayar da taji Diana nayi ana saura kwana uku abun ya faru da murmushi da con pedants, dinta ta fara bada amsa Ranar jumu'a da misalin karfe 6 da minti 16 ,na fita daga cikin gida nayi hanyar gardin don na je nasha frish air shigana wurin ke da wuya naga Diyana tana waya da sauri na koma gefe inda bazata ganniba na la6a naji tana cewa Eh tunani nake ko muyi kisan ko kuma mubi umarnin abun da dady ya fada mana amma takardu kam duka na gama dauka saura na company din da Ake jakan kuna shine kawai na rasa inda ya Ajiye shi, furucin Diyana sun daure min kai da har nayi niyyar fadawa daddy kuma dai sai na fasa niyi alkawarin gano manufar ta, haka barrt Sununsi ya dunga tambayn ta, tana bashi amsa .Bayan ya gama brrt Abbas ya soma nashi Malam Noor kince kinji Diyana tana waya da wata kuma tana kiran zasuyi kisa kinsan wasuke nufin zasu kashe? Kuma kinyi inani da Allah susuka cakawa Alhaji tafida wuk'a ?Kuma kinsan dawa take waya?kuma da sauri brrt Sunusi ya muke yace Objection my lord, kallon barrt Abbas kuliya, yayi ka gyara kalaman ka, murmushi brrt Abbas yayi yadan rusuna yace ok my lord ,ya cigaba da duban Noor Ko zaki iya sanar da kotu cewa kin tabbata Diyana Akan Abun s.s tafida take magana? Eh na tabbata Akan shi take magana, mey hajjarki na fadin hakan? wike wike tayi lokaci guda taji ranta ya 6aci ba ita ba har Barrt Sunusi saida ranshi yayi dubun 6aci da tambayoyin Barrt Abbas da sauri barrt Sunusi ya kuma mikewa tare da fadin objection my lord! tambayoyin barrt Abbas sunyi mata tsauri zata iya riki cewa , kallon sa kuliya yayi yace hakan shine daidai A sukwane Barrt Sunusi ya zauna, haka dai Noor ta gama Amsa tambayoyin, bayan haka barrt Abbas ya koma ya zauna, Barrts Sunusi ne ya fito ya ce yame girma me shari'a inaso kotu ta bani damar magana da d'aya daga cikin wainda Ake tuhuma da laifi, kan kuliya a kasa yana wasu rubuce rubuce saidaya gama sannan ya dago yace kotu ta baka dama "tnx my lord yadan rusuna kadan ya fada, komawa yayi 6angaren da su Malika ke zaune ya nunata da hannun Malam Malika barin dan miki wasu tambayoyi , bincike ya nuna cewa hannunki ne ya chaki Alhaji Tafida, Kuma a tambayar da Aka miki ki cenza suna A gidan Alhaji tafida saka makon karyan aiki da kikajeyi gidan, ko kina da hajjan yin hakan??

Kallon kuliya tayi da sauri takoyi sa'a ita yake kallo da sauri ya girgiza mata kai Alamar ta bada Amsa ,maida kallonta tayi kan barrt Sunusi tace ina da hujjan yin haka hujjana kuwa shine kar S.S Tafida ya ganeni shi yasa na cenza suna, maganar caka wuka kuma bani bace babu hannun a ciki nima haka na samu.Taya za'ayi mu yarda da hakan bacin bincike ya nuna kece? kuma munaso muji dalilin zuwanki gidan Alhaji tafida daukar *FANSA*?

Hawaye ne suka fara kwaranya daga idon ta yau zan sanar da duniya dalilin zuwana gidan S.s Tafida daukar *FANSA*, yau zan fadi abunda ya jima yana damun zuciyata, yau zan fadi abun da S.s Tafida yake 6ayewa shekara da shekaru kar duniya ta sani Dama ance ranar wanka ba'a 6oyan cibiya S.S Tafida azalumu ne, macuci ,maci amana, fasiki, S.s Tafida shine mutumin daya rabamu da farin ciki a rayuwa ya rabamu dajin dadin rayuwa, Allah ya isa tsakanina dashi tana kuka tace yanzu zan baku labarin tundaga farko har karshe

Wata rana rana mafi muni a garemu ranar dabazan ta6a mancewa dashi a rayuwata ba, ranar da muka fara fuskantar matsala a rayuwa.....

Tow masu karatu kubiyo dija zuwa gobe donji cigaba bani da chargine shiyasa kukaga na tsaya anan

Love you all❤❤❤❤
[3/2, 15:56] Khadeeja Waziri: □□□□□□□□□
FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dija_waziri

Dedicated to all my fan's

(P. W. F)

Page

77&78

Ranar Asabar da misalin karfe 7 na safe ,aka kira mahaifinmu a waya' akan yaje shugaban k'asa na neman shi cikin gagawa haka yabar cin abincin ya tashi ya tafi , kiran shugaban kasa ,bayan sun gama ta'taunawa dashi ,ya tashi ya tafi bai zarce ko ina ba sai gidan S.S Tafida, yaje sukasha hira sosai kuma suka dan ta'tauna akan takaran govnor da mahaifina ke nema, A lokacin dazai tafine Alhaji Tafida ya dauko wasu kwan zabi guda hudu dafafu ya bashi kasan cewar yasan mahaifina dason dafafan kwai , ba musu yasa hannun ya kar6a ya tafi gida.....

lokacin da yadawo gida , ya samu muntafi makaranta nida kanwata Zara da Ahlam shinkafa yasa mummyn mu ta dafa masa ya hada da kwan zabin yaci saida ya cinye kwoyin duka hudin har yana yiwa mama tayi, tace bataci kasan cewar ba cimarta bane, yana gamaci yaji kanshi ya fara sara masa haka ya tashi ya shiga daki ya kwanta yasha magani ko zaiji saukin ciwon kan.....

Sunan mahaifina Alhaji Salisu Naira, gogagen Dan siyasa ne, ya dade a siyasa sosai kuma yana da tarin arziki tun kafun ya fara siyasa , su biyu mahaifinsu ya haifa, shida kaninshi Alhaji jamil. Alhaji jamil yana da yarin ya guda daya Ahlam, shi kuma mahaifinmu biyu nida kanwata Zara.....

Mun tashi cikin gata da soyyar iyaye, babu abin da muka nema muka rasa, duk abun da mukeso shi ake mana, duk da irin gatan da iyayen mu ke nuna mana baihanasu bamu tarbiyya mai kyau ba.....

S.s Tafida aminin baban mune kut da kut tun suna samari suke abota bashi da abokin shawaran daya wuce shi babu abin da S.s Tafida bai saniba akan dukiyar mahaifin mu.....

S.s Tafida bashi da arziki amma yana da rufin asiri mahaifina ke taimaka masa da wasu dawainiyar gidan shi , kamar biyan kudin makarantan yara, kudin wuta duk shike masa ,sabida bashi da karfi sosai wani sain har cefane shike masa.....mahaifina ya yarda dashi sosai kuma baya tunanin zai iya cin amanar sa ko bayan ransa shi yasa yake Alfahari dashi.....

S.s Tafida yakan nuna masa hassada kiri kiri amma sam baya ganewa ,barin daya fara harkan siyasa Abun baiwa S.s tafida dadi ba kanin shi yakan sanar dashi cewa S.s tafida bason tsakani da allah yake masa ba kudin shi yake so kawai , Amma mahaifina ya nuna rashin jin dadin furucin kanin nasa har ya kusa ya zama musu gaba , tundaga wannan lokacin kanin yayi alkawarin bazai sake fada masa gsky akan batun S.s Tafida ba, ya zuba musu ido kawai.....

A kwana a tashi mahaifina yayi karfi a siyasa har ya fara takaran neman sanata, cikin ikon allah kuma ya samu da taimakon talakawa da suka san zaiyi masu aiki tsakani da allah, don kowa yasanshi a garin mai tausayi ne dason taimako, hakan yasa besha wata wuya gurin lashe kujeran ba , yana hawa ya bawa S.s Tafida aiki me tsoka amma sam S.s Tafiba hakan be masa ba.....
[3/2, 17:30] Khadeeja Waziri: Haka sukayi ta rayuwa burin Alhaji Tafida yasan yadda zeyi ya malaki kudin mahaifin mu, kwatsam wata rana yaje wurin sana'ar sa wato caca don Alokacin bashi da wata sana'a daya wuce caca da shan giya....

Fashewa da kuka hajiya khadija tayi da taji furucin malika, don dukda ta tsani S.s tafida bata so a fadi halinsha na daba a idon yaran shi ,waiya zubillaha ubangiji ka rabamu da uba irin S.s Tafida....

cigaba da labari m
Malika tayi caca da shangiya sune sana'arsa a lokacin suna zaune suna caca kwatsam wani inyamuri kato ya shigo wurin, da suke nan ya zauna sukayi cacan da S.s Tafida, nan S.s Tafida ya lashe duk wani abu da inyamurin ya saka, da mutumin yaga cewa S.s Tafida shegen kansane sai ya jashi gefe ya sanar dashi akwai wata harka dazai shigar dashi , wanda zaiyi kudi a tashi daya amma suna da sharuda Jikin S. s Tafida har wani 6ari yake ,da yaji ance zaiyi kudu cikin gagawa yace koma wani irin sharadine zai bi , nanfa wannan inya murin yayi wani shiumin murmushi sannan ya bawa S. s Tafida adress dinshi yace karfe shabiyun dare yazo ya samesa, sai suje gurin ba tsora ya kar6a sukayi salama ya tafi....

Haka ko akayi lokacin da mutumin yace su hadu ko minti daya bai karaba, suka hadu nan suka shiga mota suka dauki hanya, tafiya suke S. s Tafida yaga tafiya taki k'arewa har ya soma jin tsoro ,daga bisani kuma yaga sun doshi wani farin gida hadade horn yayi mai gadi yazo ya bude masa suka shiga, suna shiga yaga manya manyan jifa jifai a fake a cikin gida shidai ya tsorace ya fito suka shiga cikin gidan, saida suka wuce manya manya faluka wanda suka gaji da haduwa wurin guda goma sannan suka doshi wani daki wanda yake a kulle, saida mutumin ya kwan kwasa sannan suka bude suka shiga S. s Tafida bai tashi jin tsoro ba, sai dayaga wasu mutane da yawa a zazaune duk jikin su sun saka jajayen kaya , sunyi layi suna zaune

gaban su wani Han kacif da kwai a cikin sa guda yaya sai ogansu da yasha gashin doki fuskar sa ba ken gani.....

Matsawa inyamurin yayi kusa dashi ya fada masa abu a kunne ,sannan daga bisani yace ss tafida ya matso kusa nan suka sanar dashi dokokin su da kuma abun da suke bukata, shine ya kawo wannan aminnin nasa da yake ji dashi babu musu yace an gama sukace sun bashi shekara uku sannan zasu dauke aminin nasa.....

Tow S.s Tafida kudi sun fara shigo masa babu aikifari bare na baki , abun na bawa mahaifina mamaki amma sam ya kasa tambayan shi taya yake samun kudi.....

Haka dai rayuwa taci gaba har Allah yasa mahaifina ya sauka a matsayin sanata, ya fara neman govnor wannan kenan.....

tun wurin shabiyu da mahaifina ya kwanta be tashiba, har muka dawo daga makaran ta sai wurin hudu mum ta shiga don ganin lafiya, sabida baccin yayi yawa, tana shiga ta sameshi a tsugune sai aman jini yake nan danan hankalin ta ya tashi ta kira drive aka wuce dashi asibiti, likitoci sunyi iya binciken su amma sam sun kasa gane matsalar sa haka su mum suka dawo dashi gida, aka fara masa na hausa shima kamar kara ciwon ake haka mahaifina yayi ta jinya har na tsahon wata bakwai , S.s Tafida ko tunda ya fara ciwo sau uku yazo dubashi abun yayi masifar ta6awa mahaifina zuciya hakan yasa ya samu kanin shi yake sanar dashi abun dake faruwa nan kanin yace masa dama ae tuncen na fada maka kuma ni yanzu ina zargin akwai wata kulaliya a kasa ina tunani wani abun suka maka ,haba ya za'ace daga cin kwai sai rashin lafiya, akwai wani malami da mukayi magana dashi yace zai zo yau da dare ya duba ka,

Hmmm jamil kenan inaji a jikina bazan sake nufashi a duniyaba, daga yau haba yaya ka dena fadin haka insha Allah zaka samu sauki, hmm jamil bakasan ya nakejiba nidai kawai inaso ka yimin alkawari guda daya, shine bayan raina ka auri matata tunda Allah yayiwa matarka rasuwa sai kucigaba da rainon yaran mu ,duk wani abu dana malaka suna cikin nan, ya daga kasan filon da yake kwance ya dauko wasu takardu ya mika masa ka cigaba da juyasu na baka halak malam kamfanina na dubai kuma nabawa Malika, na jakan kuna kuma na bawa Rara gidan maina dake kaduna nabawa mahaifiyar su dayan dake bauchi kuma na baka ,tare da sauran dukiya ta yana kuka ya kar6a.....karfe shida malamin da Alhaji jamil ya kira yazo tare suka shiga har dakin mahaifin mu nan malamin yayi yan adu'oin shi, tare da wasu yan tofe tofen shi ya gama ya fita nan yake sanar da Alhaji jamil Cewan yan shan jini ke bibiyar ratuwar sa , so suke su kashehi yakuma basu adu'ar da zasu ringa yi masa, cikin ikon Allah zasu rabu dashi nan sukayi salama malamin ya tafi Alhaji jamil bai sanar da mahaifin mu abun dake faruwa ba kawai yayi alkawarin saiya gano gaskiya tukun haka yazo yayi wa mahaifin mu salama ya tafi....

Mun dade muna hira dashi yana tayi mana nasiha amma nasihar da yake mana tasha banban dana kullum, daga karshe kuma ya fara bada wasiya yace ko bayan ranshi kar muyi masa kuka , haka dai yayi tayi sai gurin 1 na dare mummy tace muje mu kwanta daker.....

kuka Malika ta kara fashewa dashi, cikin shasheka tace wurin karfe 4 na asuba mummy ta fito tana kuka , wayyo Allah kulu nafsin za'ikatul maut duk mai rai mamaci ne Alhaji salisu kam ya amsa kiran Allah, nan danan unguwa ta caku6e don babu wanda baiji mutuwar saba nan danan aka sanar a masalatai.....

Washe gari da wuri aka kaishi makwancin sa, S.s tafida ko jana iza bai zoba, kuma yaji duk batun.....

"Shegen janwuya naga shari'an ku na yau gsky kana kokari ,kuma naga Alamun kamar muzamuyi nasara "insha Allah mune Amma Alhaji ya kamata ka ziyarci kotu ranar biyar ga wata shene last shiga da za'ayi kuma nasan yanzu dole zasu kara bincike sosai kuma zasu gano ka samu sauki "

Dariya Ss Tafida yasa irin na shegun yan duniyar nan yace"Kurka damu zan je insha Allah me suke dashi da har zasuyi nasara 'a kaina ,ai haryau ba'a haifo wanda zaici galaba' a kaina ba.....

Kuyi hakuri da wannan typing wahala☺
[3/31, 10:49 PM] Dija waziri: □□□□□□□□□
FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dija_waziri

I dedicated this whole page to you humaira madaky tnx for the love, care nd support u meda me so happy today😊I love you so much and will never forget you in my life😍😘

(P. W. F)

page

85&86

Dariyan mugunta Barrt Sunusi yasa yace "Alhaji kana balain burgeni wlh, ae sukansu lawyas d'in wainda ake tuhuma da laifin sai da nace su hakura, amma sunki, ae shi Barrt Abbas yasan waye ni, shi yasa bai cika tankani ba, wata mataimakiyar sace wadda kwata-kwata bata jima da fara 'aiki ba take son ja dani".....

S.s Tafida ne yace "tow aci uban ta mana nawa take kwata kwata, kuma waye ita' a k'asar nan me take dashi?" A'a rabu da ita kawai Alhaji Manya-manya ma sun goga dani sun bari bare wata ita karan -kad'a miya, ae zatasan dawa take ja inja nine fa Barrt Sunusi" Yawwa Barrt kaga yaranan sunaso su tozar tani ,su tonamin asiri, susa duniya ta zageni, a dena ganin mutunci na, ni Jurge Muktar d'in ma nake so a kashe saboda shima 'akwai tamu dashi," yawwa Alhaji ka kawo shawara kawai kafun a shiga karan k'arshe ya zamana munsan yan da 'akayi aka kashe shi sai Jurge Kalid ya cigaba da gabatar da shari'a, kaga inde shine ,nasan kota k'arfi sai munyi nasara".....

Ss Tafida ne yayi wani shi'umin murmushi yace "ka kawo shawara Barrt Haka za'ayi yanzu ka samo wanda zamu biya su mana aikin kow" tow kar ka damu ina da yara sosai ,sudai burin su a basu bugun abuja" tow...tow ....towwww ae kud'i mai sauk'i ne a gurina kuyi ciniki dazu ko nawa ne zan biya"cewar Ss Tafida.....

****
Ab'angaren su Barrt Abbas kuwa hotel d'in da Jurge Muktar ke zaune suka nufa dukkan su zuciyoyin su cike da tsoro ,suna shiga suka tadda Jurge muktar sai kaikawo yake a tangamemen d'akin daya sha royel bed, Hajiya ko na kan gado tayi tagumi shigar sune yasa Jurge Muktar tsayawa da kai-kawon da yake cikin 6acin rai ya kalle su yace.....

"Haba Abbas yanzu abunda kukayi yau a kotu ya dace kenan?" Had'a hannayen shi Barrt Abbas yayi wuri d'aya cikin kunan zuciya yace"am so sorry sir wlh ba da gangan hakan ya faru ba, sai da mukayi dasu zasuzo duka shedun namu, kuma suka amince , ita kuma Hajiya Asabe munyi yarje -jeniya da ita kuma ta 'amince zata ziyarci shar'an ,sai kuma mukaga ta koma bayan su Barrt Sunusi"...

Mik'ewa Jurge muktar yayi daga zaman da yake yace" Abbas !Minal !dole fa mu tashi tsaye akan shari'anan idan ba hakaba wlh bazamuyi nasara ba, saboda bamu da k'awaran shedu ,ina so kuziyarci hospital din da Ss Tafida yake ku gano min yasamu sauk'i ko kuma har yanzu jikin dai, don gsky ban yarda ,da doctor din shiba " Tow sir insha Allah zamuyi iya k'ok'arin mu " cewar Barrt Minal.....

Tow abubuwa dai sun fara tafiya wa su Barrt Abbas yanda ya kamata ,kuma sunyi bincike sun binciko cewa Ss tafida ya mik'e.....

Yau talata saura kwana uku a koma kotu, Judge muktar ne zaune cikin d'akin su yana duba wasu yan takardu ,wayan shi ya fara ruru glass dinshi ya dauko yasa, ya duba wayan don yaga me kira number ya gani ba suna, cikin nutsuwa ya d'aga da salama, daga 6angaren wanda 'ya kira ne ya fara magana kamar haka....

"Hello Jurge Muktar ne?"

Daga 6angaren Jurge Muktar yace "Eh shine waye?"

Dariya mutumin yasa yace"bana so muyi wani dogon zance da kai ,ina so kazo bayan irfan petroleum ,ina jiran ka kuzo kai da Barrt Abbas zan sanar daku komai na game da Ss Tafida kuma ,dic d'in da kuke nema yana wurina ,nabaku nan da 'awa d'aya kuzo ku sameni".....

Kubiyo ni 😊

Love you all my fans😘
[3/31, 10:49 PM] Dija waziri: □□□□□□□□□
FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dija_waziri

Na sadaukar da wannan shafin gareki Rukayya Ibrahin Kofa tnx four the zumunci😍😘

Ya Allah kazama gatanmu ka karemu aduk inda muke ka bamu juriya da dangana. Ina Alfahiri daku masoyana Allah ya barmun ku❤❤❤

(P. W. F)

Page
87&88

Barrt Minal ce zaune kan kujera' a holet d'in dasu jurge Muktar suka kama, sai faman kiran Wayan Barrt Abbas take amma akashe , hankalin ta duk ya tashi, hajiya ko na zaunebakin gado ta zabga uban tagumi duk wanda ya kalli fuskar ta yasan tana tsananin damuwa.....

Barrt Minal ce ta nufo inda take tace "Hajiya kinji wayar tasa ma 'a kashe kuma jiya da dadare muna cikin waya dashi naji ya katse wayan kuma nayi ta kira yana ringin aman ba'a daga ba, ko sanda oga zai fita ya sanar dake inda zashi?"

Hajiya tana zubar da kwala tace"gsky be fad'amin ba cewa dai kawai yayi min bari suje su dawo shida Barrt Abbas" tow ina suka shiga kenan? Bari mubari muga ko zasu dawo zuwa anjima cewar Barrt Minal.....

Haka sukayi ta zama suna jira har wurin k'arfe 5 na yamma Barrt Minal tana hotel din bata tafi ba kuma basuzo ba basuyi waya ba kuma ,ita kam Hajiya harta sadak'ar wani abun ya samesu ne don hankalin ta yak'i wanciya sam.....

Barrt Minal ce ta mik'e ta d'auki mayafin ta tace "hajiya nikam barin je nayi cikiyar su duk yanda akayi akwai abun daya samesu ,ace tun jiya da dare ba'aji duriyan suba har aka wayi gari gashi kuma wani daren ne zai kumayi ,yanzu gsky da ,alamar tmby a lamarin su"

Hajiya ce tace "tow Minal dan Allah atemaka kinga shi kad'ai nake dashi a duniya"insha Allah za'a gansu Hajiya ki kwantar da hankalin ki" cewar Minal....

Barrt Minal harta bud'e kofa zata fita taji wayanta ya fara ruri da sauri ta duba taga Barrt Abbas ne ta daga cikin sauri ,Abun da ya fad'a mata ba karamin razanata yayi ba bata san sanda ta furta, *innarulahi wa inna ilaihi rajiun ba* tsabar razana....

Da sauri Hajiya tayo gunta tana" lfy meya furu Minal inace dai lfy kow?" Kallon ta Minal tayi tana mai zubda hawaye tace, "ba lfy ba hajiya I'm sorry to seay "kuma sai tayi shiru ta kasa furta abun da zatace, kuka hajiya ta Saki me tsuma zuciya tace"Minal ki fad'amin meke faruwa?" fuskar Minal da tajuya ta koma jazur abunka da faran mace ta d'ago idanun ta da suka rune suka koma jazur cikin k'an -k'anin lokaci ta sauke su kan hajiya tana inda- inda tace "Hajiya duk abun daya samu bawa ya daukeshi a k'adara ina so ki zama mai juriya da tawakali da yadda da k'adara ina so kisan wannan abun daya faru k'adara ce da jarabawan ubangiji" kallon ta Hajiya tayi cikin 6acin rai tace "Minal ki fad'a mun meke faruwa "

Hajiya sai dai kiyi hakuri Jurge Muktar ya 'amsa kiran Allah, Innarilahi wainna ilaihi raji 'un Allahuma Ajurni fi musibatan,shine abun da Hajiya ta iya furtawa yayin da ta fad'i k'asa 'a sume , Barrt Minal na ganin haka tasa ihu cikin gagawa ta fice tayi ta kira mutani suzo su taimake ta, cikin gagawa suka zo aka dauketa sai asibitin....

Wani asibiti suka nufa cen wajen gari cikin gagawa doctors suka,kar6eta.....

Barrt Minal kow duk ta rikice ta rasa 'abun dake mata dad'i, zaune take kan wani kujera ta had'a kai da cinya tana hawaye me cike da bak'in ciki , d'agowan da zatayi kawai taga Barrt Abbas zai wuce , da sauri ta mik'e tasha gaban shi tana kiran sunan shi "Barrt Abbas meya kawoka asibitin nan?" Yana ganin ta yaji wata fad'uwa gaba ,bai san sanda shima yace mata"meya kawoki nan Barrt Minal?" tana hawaye tace"Hajiya ce tafad'i lokacin da nasanar da ita mutuwar Jurge Muktar"ya salam yanzu tana ina ne?"cewar Barrt Abbas.....

"Tana cen d'akin" ta masa nuni da hannun ta ,tow barinje na dawo kafunnan doctors d'in sun fito, tsaida shi tayi da tmbyn "Barrt Abbas ina gawan Alhaji Muktar anan asibitin ya mutu?".....

Tambayan Barrt Minal ce yaji tazo masa 'a bazata ,shiru yayi bai ce da ita komai ba ,sai da tasake tmby snn ya ce mata"ae har anyi masa salla d'azu da safe an kaishi", mamaki abun ya bawa Minal sosai ya za'ayi ace ankaishi bayan ba bari iyalan sa ,sun ganshi ba 'anya 'akwai k'anshin gsky cikin maganar Barrt Abbas kuwa?" (Tow nima dai dija abun ya daure min kai amma kucigaba da saurarona

masu karatu) da tunani barkatai Barrt Minal ta rabu da Barrt Abba tare da tambayoyi mak'il cikin zuciyar ta.....

Tow bari mu lek'a asibiti gurin su Ss Tafida muga sukuma wani plan din suke had'awa.....

Zaune yake ya hakince kan gado yana karanta jarida kamar yanda ya saba ,kusa dashi kuma wani d'an jarida ne ,sai kuma Barrt Sunusu, suna tatauna yanda zasuyi gobe a kotu Barrt Sunusi ne yace....

"Ae wlh zan nunawa Barrt Abbas waye ni gobe Ammafa Alhaji wlh daren jiya da sai naga kamar akwai wanda yake binmu cikin dan dajin nan fa don lokacin da aka kwad'a masa itace naga giftawan mutun"

"Ae tunda aka kashe Muktar anyi mai wuyar don ko gobe mu zamu cinasara 'a kotu"cewar Ss Tafida.....

Karfe 5 da rabi na yamma Hajiya ta tashi babu abunda ta fara tmby sai ina Alhaji ? Cikin kulawa Barrt Minal ta kalleta tace"kiyi hakuri hajiya dukkan tsanani yana tare da sauk'i jarabawa ce Allah yake jarabtan ku dashi Ubangiji Allah ya baki ikon cin jarabawan" Hajiya na kuka tace ameen Minal nagode ,da shawaran da kika bani insha Allah zan cigaba da hakuri Akan wanda nake yi Amma ninasan bazan sake fuskantar farin ciki a rayuwata ba, bani da kowa sai Allah ubangiji Allah ka nunamin Fadil d'ina".....

"Ameen Hajiya kidena cewa kinyi ban kwana da farin ciki ,baki san me Allah ya tsara miki nan gaba ba, kuma wlh duk wanda ya zalunci wani Allah baya ta6a barinshi ko bajima ko badad'a Allah saiya bimiki hak'in ki,"cewar Minal.....

"Hakane Minal kinyi gsky" tana kuka tace "Allah ya jik'an Alhaji yanzu ina wagan yake?" Barrt Minal tace Ameen d'azu muka had'u da Barrt Abbas yace min wai tun d'azu da safe aka masa wanka aka kaishi" ban gane ba Minal ya muna gari d'aya 'amma 'ace mijina ya rasu kuma an binne shi ban ga gawan shiba? Anya akwai k'anshin gsky kuwa?" Tow nima dai abun ya daure min kai ,kuma Barrt Abbas d'in yace min zai dawo amma har yanzu bashi ba lbrn shi ,kuma gashi gobe zamu shiga kotu ga wayan shi yaki shiga".....

"Tow kow wlh bazan yarda ba wannan munafurci ne wlh zansa matakan tsaro suyimun binciki"cewar Hajiya.....Minal ce tace Hajiya kar ki damu insha Allahu ni zanyi bincike sai nagano abun da 'ake son 6oye mana" tow Allah ya mana jagora nagode da kulawarki a garemu" cewar Hajiya....

Kafun waye war gari k'asa duk ta d'auka cewa Jurge Muktar ya rasu Abun ka da manyan mutane , dalilin hakan yasa 'aka d'aga shari'a sai bayan kwana uku lokacin da lbr yaje kunnen Malika sai da tasufa wurin sau 3.....

Barrt Abbas ne zaune cikin wani gida ginin dutsu yana bincika wasu takardu gefen shi kuma wani babban mutun ne kanshi nad'e da bandeg yana zaune kan sofa ya mik'e k'afa yana karatun jarida, sai kuma wani mutun sai zubamusu surutu yake ga dukkan Alamu d'an jarida ne, wayan Barrt Abbas ne ya fara ruri da sauri ya duba yaga Barrt Minal, rubuce jikin screen d'in wayan ,da sauri ya d'aga kanshi ya kalli wannan mutumin yace sir.....

Kubiyo dijawaziri dan jin cigaba.....
[3/31, 10:49 PM] Dija waziri: □□□□□□□□□□
FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□□

Story /writing by dija_waziri

~This page gost to you my k'awas Rookiey, and miss Aisha thanks for this love, care nd support really appreciate it 😍love you guys~ □

(P. W. F)

page

87&88

Yana kashewa Jurge Muktar yayi dailing number din Barrt Abbas bugu d'aya ya daga, nan ya sanar dashi yazo hotel ya sameshi akwai inda zasuje ,ya kashe ya fara shiryawa, shiko Barrt Abbas shiru yayi yana tunanin ina zasuje haka wurin k'arfe 12:40 na dare, da wannan tunanin ya tashi ya shirya ya fice,

A bakin kofar hotel d'in Barrt Abbas ya tadda Jurge Muktar ,yana ganin Barrt Abbas ko gama paking beyiba ,yaje ya bud'e k'ofar motan ya shiga yace"juya mu tafi irfan petroleum akwai wanda ke jiran mu yanzu ,kuma kayi sauri"......

Shidai Barrt Abbas Abun ya d'aure masa kai, aduk sanin shi da Jurge Muktar baya fita bayan sallar isha amma gashi wai yau zai fita wurin k'arfe d'aya, da tunanin hakan suka isa wurin, dajine kuma duhu dulum babu haske a gurin, Babu 6ata lokaci Jurge muktar ya kira number dugu d'aya mutumin ya daga yace.....

"Kuna ina ne ?"

Cikin rawan jiki judge Muktar yace "muna bakin titi gefen irfan"

Dariya mutumin yayi irin da yan duniyar nan ,hahaha...."tow kufito daga motar ku shiga cikin dajin dazu gannin".....

Da sauri Jurge Muktar yace tow gamunan , hanzarin bud'e kofa ya somayi ,da sauri Barrt Abbas ya rik'o masa hannun "oga , inaji a jikina akwai abun dazai faru ka bari ni kadai naje" kallon shi Jurge Muktar yayi , yace "haba insha Allah ba abun dazai faru taimakon mufa zaiyi tashi kawai muje"kafun Jurge Muktar ya gama ida abun da zai ce sukaga giftawan wani mutun , nan Barrt Abbas yace "ok sir jeka ina zuwa barin kira , baik'arasa fadin abun dazai ceba Jurge Muktar yace "kul karka soma nidai barin je kazo ka samen ya bude kofar ya fice....

Shiga cikin dajin yayi tafiya yake yana haska touch light din wayan shi amma sam bega kowa ba, sai da yayi nisa da bakin titi sosai sannan ya soma ganin harke cen cikin dajin, har gurin hasken ya isa bega kowa ba ,annan ya tsaya ,yafara dailing number din mutumin ringin yake sosai amma ba'a d'aga ba sai da yakira shi har sau 6 da 'amma sam babu alamar za'a dauka ,cikin jin haushi ya juya da zumar tafiya sai tsaki yake ,juyawan da zaiyi yaga wani mutun mara ken gani kanshi buzu buzu yana

masa dariyan mugunta , juyawa yayi zaibi ta dayan hanyar ya wuce namma yaga wani ya nufoshi da bindiga A hannun shi ,salati ya saki ya kuma bin wata hanyar don ya tafi be ankara ba yaji saukan wani k'aton itace a kansa ,juyawa wurin ya soma masa, nan danan yaga gurin ya fara juya masa ya fad'i agun tim, yana mai kiran sunan Allah...

Shigo Barrt Abbas duk bai san wainar da 'ake toyawa ba don yana cikin mota yana waya da Barrt Minal ,jin k'aran bindiga ne ya sashi saurin yasar da wayan , ya d'auko wani bindiga a cikin motar yayi cikin dajin da sauri,

Innarilahi wainna ilaihi rajiun shine abun da ya furta yayin da yaga jurge muktar kanshi na zubar da jini kuma yana kwance ko motsi baya yi, gashi bai tadda da kowa a wurin ba, jijigashi ya somayi yana"sir mesuka maka sir "amma yaji shiru cikin gagawa ya daukeshi sai hospital.....

Kuyi hakuri da wannan zuwa dare insha Allah zan cigaba muku daga inda na tsaya bani da time ne yanzu😊

I hope you enjoy reading it ☺

Sai naji comments d'inku
[3/31, 10:49 PM] Dija waziri:
FANSA

REVENGE

Story /writing by dija_waziri

I dedicated this page to my lovely mother, I love you so much ❤Allah ya k'ara miki lfy da nisan kwana da shekaru masu Albarka, Allah ya barmin ki ina Alfahari dake uwata ta kaina❤bani da abunda zan iya saka miki dashi sai addu'a da fatan Alkairi A rayuwa Allah na gode maka da kabari uwa tagari mai k'aunata ☺ina 'alfahari dake mahaifiyata farincikin rayuwata Abun Alfaharina❤😍😘

(P. W. F)

Page
89&90

Barrt Abbas ne zaune cikin wani gida ginin dutsi yana bincika wasu takardu gefen shi kuma wani babban mutun ne kanshi nad'e da bandeg , yana zaune kan sofa ya mik'e k'afa yana karatun jarida ,sai kuma wani mutun sai zubamusu surutu yake ga dukkan Alamu d'an jarida ne, wayan Barrt Abbas ne ya fara ruri da sauri ya duba yaga Barrt Minal ,rubuce jikin screen d'in wayan , da sauri ya d'aga kanshi ya kalli

wannan mutumin yace "sir nifa na rasa yanda zanyi da Hajiya da Barrt Minal ,sun sani a gaba fa ,suna ganin kamar bani da gsky tun shekaran jiya ta damen da kira, gashi yanzu ma ita ke kira".....

Rufe jaridan dake hannun shi yayi ya d'ago da kanshi yana wani murmushin daya k'ara fito da kensa kamarsu d'aya da fahad,(ni dija dana ganshi saida birona ya fad'i tsabar mamaki wai Ashe judge Muktar be mutu ba□tow miye dalilin da yasa ,sukace yamutu? Muje zuwa masu karatu) yace"kar ,ka damu daduk abun da zasu cemaka, kuma ban yarda ka sanar dasu cewa ina raye ba, ni Jurge Muktar zan nunawa Ss Tafida cewa wayon shi kad'anne da nawa shi kuma Barrt Sunusi yabar aikin low kenan har abada wlh!! Munriga da munyi magana da Jurge Abdul akan ya yarje musu zai kar6i karan ya cigaba , amma nidana fara nizan cigaba ,ae su duk basu san aminina neba"..

Wannan dan jaridanne yayi dariya,yace "gsky Alhaji Tafida sam bashi da woyo ko kad'an, saboda duk abun da zaiyi ina zaune a gurin yake yi baya tsoran wani aba, ranar da suke maganar kasheka basusan ina record ba"....

Barrt Abbas ne yace "Hmm ae ni aduk cest d'in da nake ,kar6a na mutane ,dayawa ban ta6a ganin mugun mutun irin Ss Tafida ba ,haka zalika 'aduk lawyas d'in da muke hurd'a dasu ban ta6a ganin makiri irin saba ba".....Haka sukayi ta hira tare da shawara 'akan yadda shari'a zata kaya jibi.....

A 6angaren su Hajiya kuwa duk sun gama sakan -kan cewa Judge Muktar ya rasu, Barrt Minal kuwa nanan, na bincike,

Fahad ne zaune wani falow d'an madai-daici wani dan k'areren carpet ne kawai shinfid'e a ciki sai pillows yan k'anana da aka jera kan carpet d'in ,sai tv dake manne jikin bango yana kallon ajazeera, mutanen dake tsare dashi ne suka cenja tashar zuwa bbc hausa ,ganin poton Ss Tafida ne yasashi gyara zama donjin labaran da kyau....

An d'aga sharian Ss Tafida da wainnan yan matan zuwa kwana uku,saka makon rasuwan babban Judge me adalci da 'ake ji dashi a k'asar nan wato Judge Muktar!! Wanda dama shike wakiltar shari'an, suka nuno k'aton pictur d'in Judge Muktar.....

Fahad yana daga shingid'e saida ya tashi zaune ,yana kallon abun mamaki yau yaga me kama dashi ,tare da tunanin meya samu Ss Tafida har ake shari'a dashi ,kuma suwaye yan matan?

Kallon wa innan gardawan dake gadin sa yayi cikin muryan tausayi yace"dan Allah ku sakeni na tafi ni ban san miye manufar ku na 'ajiyeni anan ba," kafun mutanen su furta 'abun da zasuce ba sukaji murya daga bakin kofa ana cewa ,

"Taimako yasa muka d'auko ka bamu d'aukeka don cutar dakai ba" yana magana yana cigowa....Fahad na ganin shi cikin tashin hankali da mamaki ya mik'e , ya fara nuna mutumin da yatsa yana "dama kaine?".....

Da murmushi mutumin yace nine basai ka k'arasa ba fahad nine ,"nasan zakayi mamakin ganina sosai, bazan iya baka lbrn komai yanzu ba 'amma ka kwantar da hankalin ka zakaji komai".....

Shidai fahad sakin baki yayi kawai yana kallon shi, har yazo ya zauna yace da mutanen sud'an basu wuri suyi magana.....

Suna fita mutumin ya fuskanci inda Fahad yake ya fara magana kamar haka" ina rokon gafarn ka Fahad, ban ta6a tunanin haka zai faru ba, shi yasa banyi saurin bayyana kaba , na d'auko ka nanne badon komai ba,sai don taimako ,sabida naga irin wulak'anci da Ss Tafida ya maka"..

Cikin rashin fahimta Fahad yace "ban gane ba nifa kasani a duhu" murmushi mutumin yayi yace "Fahad wannan bawan Allah dakaga 'anuna Jadge Muktar Mahaifin kane shiya haifeka" Fahad bai san sanda yace "what" ban ganeba kana'nufin kace shine yahaifeni kuma ya wulak'an tani ya yasar dani? Innarilahi wainna ilaihi rajiun Amma banyi sa'an iyaye ba 'ai yau koda ace ni shege ne bazasu min haka ba".....

"Dena fad'ar haka Fahad kar kayi musu fasara irin haka , yau zan baka lbrn yadda 'akayi aka rabaka da iyayen ka" nan ya kwashe lbr tas ya bashi.....

Fahad yana kuka yace "wlh ! Wlh!! Ni Fahad sai na kashe Ss Tafida , Allah sarki naso nasan iyayena amma 'Allah beyi zan gana da ubana ba" wani shiumin murmushi mutumin yasa yace "ashe masu d'aukar *fansa* suna da yawa"

Kallon shi Fahad yayi yace "ban gane ba kana nufin kace min bani kad'ai bane?" Eh ae kai naka ruwan k'an-k'ara ne akan nawasu kai naka ba komai bane, ae yanzu haka ma 'anshiga kotu ana shari'a".....

Ya Allah "dan darajan Annabi kabarni nafita anan yau" cewar Fahad

"kayi hak'uri Fahad zan fitar dakai amma bayau ba, Akwai wani buri da nake son cikawa nan da kwana biyu" fad'in burin da yayi ne yasa fahad tunanin malika ,lokacin da tata6a furta masa irin haka, azuciyar shi yace Allah sarki Diyana nasan yanzu kin koma garinku ina sonki har yanzu, I love you my angel so much Allah ya nuna minke.....

A b'angaren Malika ma ta takure guri d'a duk abun duniya' ya dameta, don tunda 'aka cemata Judge Mutar ya rasu ta dena jin dad'in komai nadaga rayuwan ta, kwance take, kan katifan su tana ta tunane tunane barkate tana hawaye, Fahad ne ya fad'u mata arai ta tuna randa yake cemata, i love you wani sabon kukan ta kuma fashewa dashi ta fara magana 'a zuci wanda bata san ya fito fili ba "I love you too yayana i love you and miss you dearly i know you miss me too. Please come back to me....ya Fahad ninasan bazan ta6a zama matar kaba, rayuwata bata da amfani, a yanzu mutuwa zanyi "....

Jin magan ganun da Malika keyine yasa su Ahlam saurin yowa kanta ,suna kuka sukace "haba Sis karfa ki manta dukkan tsanani yana tare da sauk'i ,ki dena fad'in rayuwarki bata da 'amfani",Hmm bazaku gane bane ni nasan bazamu ta6a yin nasara a shiga kotun gaba ba kuma za'a iya cewa za'a had'amu duka a kashe ,ni kuma bazan ta6a son hakan ba, zanso ace kuku zauna kuga yanda k'arshen azalumi Ss Tafida zai kasan ce, malika na kuka taci gaba da cewa zanyi sicrifising life d'ina sabi daku zance ni ce na kace Rabi " Wlh bazai yuwu ba Malika bazan ta6a yarda a kasheki ba, bayan bake kika aikata ba wlh saidai a kashemu duka bazan iya kara rayuwa a duniya idan har aka kashe keba" Ahlam ta fad'a tana kuka. Zara ma tace itama sam bata yarda ba, haka sukayi ta jain ja da Malika har ta hak'ura ta rabu dasu.....

Tow rana dai bata k'arya yaune ranar da za'a cigaba da gudanar da shari'a, kotu ya cika dam da jama'a don yau jama'ar tafi na kullum, lawyas duk sun zo, Ss Tafida ma ya je yau , tsakanin Barrt Abbas da Barrt Sunusi babu abun dake tsakanin su sai hararan juna,Barrt Sunusi sai dariyan mugunta kawai yake musu, tare da jifansu da wani irin kallo.....

Tow kotudai yayi shiru shigowan kuliya kawai ake jira.....

Tow masukaratu ku kasance tare dani don jin cigaba.....
[3/31, 10:49 PM] Dija waziri: □□□□□□□□□

FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dija_waziri

NASADAUKAR GA SHIFINNAN MA FAMILY D'INA WAZIRIS FAMILY ALLAH YA BARMUNKU SISTERS AND BROTHERS D'INA INA ALFAHARI DAKU 😍😘

SECOND TO THE LAST PAGE

(P. W. F)

Page

91&95

Tow kotudai yayi shiru shigowan kuliya kawai ake jira , Ss Tafida kow sai washe baki yake kamar gonar auduga, Hajiya Khadija da taji cewa Ss Tafida zai zo sai tak'i ziyartar kotun....

Su Malika kam na tsaye wurin da 'aka tanadar musu ita da sauran yan uwan nata da duk tsoro ya kamasu, ganin Ss Tafida , Malika kam kanta na sunkuye sai zubar da kwalar bak'in cikin rashin mutuwar Ss Tafida take, Hajiya matar Judge Muktar da sauran yan uwan tama zaune suke sunyi jugun jugun babu wani mai wal wala 'a cikin su...

Karfe 12 na cika sukaji bud'e kofar kotun kowa hankalin shi ya koma kan k'ofar, yan jarida ne suka fara shigowa tare da masu video suka nemi wuri suka tsatsaya sannan daga baya sai ga Judge Muktar ya fito daga motar shi cikin kaya irin nasu babu abun da yake said murmushi tare da d'agawa mutane hannu, ya nufi cikin kotun ,kafun ya k'arasa har Ss Tafida sun hango shi, wani gumi Ss Tafida ya fara jin yana karyo mishi shiko Barrt sunusi hular kanshi ya cire ya fara cizon yatsa.. Yana kara sowa kotu ta kaure da surutu tare da mamakin da alajabi , sanda malika ta hango Judge Muktar bata san sanda tayi saurin rugawa inda yake ta rungume shiba , wayyo dad'i kuzo kuga irin farin cikinda family din Jurge Muktar suka tsinci kansu ciki , mara fusal tuwa (ni kaina dija gefe na nema na zauna harda dan kwalana tsabar murna😊) Barrt Minal kow d'aga hannun sama tayi tana godewa Allah ....

Da k'er Malika ta saki Jurge Muktar ya tafi gurin zamansa ya zauna sannan kowa ya koma ya zauna,akayi shiru don za'a fara gudanar da shari'a

Babu 6ata lokaci kuliya ,ya bada damar cigaba da gudaran da shar'a..Barrt Sunusi kasa mik'ewa yayi don duk jikinshi yayi sanyi, Ss Tafida ko ya zuba masa ido yana jiran yaga tashin sa 'amma sam Barrt Sunusi ya kasa komai.....

D'agowa Alk'ali yayi fuskarshi dauke da murmushi da kaganshi yau kasan yana cikin farin ciki mara iya ka,yace. "lawyan wanda suka ,kawo k'ara kaifa muke jira ko baka da abun cewa ne?" A sanyaye Barrt Sunusi ya mik'e yace yamai girma mai shari'a bani da abun...kafun ya k'arasa furta abunda zai ce Ss Tafida ya tashi cikin zafin, nama yace "kar ka raina mana hankali mana ya zakace baka da abun cewa bayan ga shedu munzo dasu" Kuliya ne ya buga kundin gaban sa yace "Tafida nan ba gurin fad'a bane ka bari idan kun fita kwayi, idan kuma kak'i kotu zata d'auki mataki a kanka".....

Cikin jin haushi Ss Tafida ya koma ya zauna, tare da cire babban rigan daya sa, yana share gumin k'anshi...

Shiko ,Alk'ali komawa yayi yacigaba da wasu yan rubuce rubucen sa, Barrt Abbas ne yazo daidai kunnen Barrt Sunusi yace "kar kayi give up mana ko ,kamanta waye kai baka wasa fa".....

Wani mugun harara Barrt Sunusi ya jefi Barrt Abbas dashi ,shiko Barrt Abbas ya bishi da wani murmushi me alamar tuhuma 'a ciki....

Sai da kuliya ya jima kafun ya d'ago yace "lawyan wainda 'ake tuhuma ko kuna da abun cewa?"

Da sauri Barrt Abbas da confidence d'insa ya mike yace Eh nan ya fita ya nemi izinin kotu da tabashi damar gabatar da shedar sa ,babu ,6ata lokaci kuliya yace "kotu ,ta baka dama"

Nan Barrt Abbas ya kira Alhaji sani , don gabatar da sheda babu 6ata lokaci Alhaji Sani ya fito gaban kotu, ganin Alhaji sani ba k'aramin rikita Ss Tafida yayi ba tare da Barrt Sunusi ,

(tow masu karatu nasan ba lalle ku gane Alhaji Sani ba tow ba kowa bane sai wannan d'an jaridan da sukayi magana lokacin da akace Judge muktar ya mutu ina fatan kun fahimta)...

Nan Alhaji Sani yayi rantsuwa da Allah akan bazai fad'i komai ba face gsky, ya kuma gabatar da kanshi snn Barrt Abbas ya fara masa tambaya kamar haka,

 "Malam Sani muna so kayiwa kotu bayanin abun da kaji su Ss Tafida suke fad'i ranar ishirin ga watan uku shekara ta dubu biyu da goma sha bakwai ,a babban asibitin dake garin abuje"....

Malam Sani da confidence d'in shi ya fara magana , "tow ranar naje hospital wurin Alhaji Tafida don na gaida shi ,tow da yake mun saba dashi sosai bayan na gaisheshi na fita zan tafi sai na tsaya wurin windon d'akin ina waya , tow Alokacinne naje suna maganar kashe Jurge Muktar sabida sun san idan sun barshi doran k'asa bazasuyi nasara ba, tow gudun kar su k'aryatani yasa nayi recoding a waya ta".....

Wani gumu Ss tafida ya faraji har kwaranya yake nan danan ya fara nadaman abubuwan daya aikata

(ohhh rayuwa kenan dama ance akwai ranar kin dillanci ,ranar wanka ba'a buyan cibiya ya ubangiji kasa duk abun da zamuyi a rayuwa ya zama munasa gsky da 'amana ka hanemu da yin zalunci da kwad'ayi da hangen abun wani ameen)

Nan Barrt Abbas ya kuma jefowa Malam Sani wata tmbyn da yasa Gaban Barrt Sunusi matuk'ar fad'uwa "Malam Sani ko zaka iya sanar da kotu cewa Ss Tafida shidawa ka samesu a d'akin ?"

"Eh wannan bame wuya bane ,shida lawyan sane Barrt Sunusi," da sauri Barrt Sunusi ya mik'e yace "wlh k'arya kake sharine kawai zaka min "yana nunashi da d'an yatsa.....

Kuliya ne ya kalleshi yace" kafi kowa sanin dokar kotu ,tow ka nutsu" nan ya koma ya zauna yana haki ,ita kuwa Barrt Minal sai satan kallon shi take tana murmushi.....

Nan Barrt Abbas ya cigaba da wa Malam Sani tambayoyi , daga k'arshe ya kar6i wayan shi yasa recod din ya mik'awa kuliya kowa yaji, mutane basai suka fara salati ba daga masu Allah wade se masu zagi ,shiko Ss Tafida ya rasa meke masa dad'i.....

Nan Barrt Abbas ya koma ya zauna , kuliya ya tmby lawyan wainda ake tuhuma ko yana da abun da zai cewa Alhaji Sani ,Barrt Sunusi ya girgiza kai Alamar A'a.....rubuce rubuce judge Muktar ya shigayi saida ya shafe wurin minti 20 yana yi sannan ya d'ago yace ko akwai mai magana ,kafun Barrt Abbas ya mik'e sukaji murya daga kofar shigowa kotu kamar haka....

"Akwai mai magana yamai girma mai shari'a gaba d'aya yan kotun suka maida han kalin su kan me magana ,Ss Tafida waze gani in ba PA din shiba, da sauri yaje inda yake ya rik'o hannun shi yana kiran sunan shi yana cewa "k'arshen karya tazo na jima ina nemanka kazo ka bada sheda amma na rasa inda zan sameka".....

Bangaje Ss Tafida PA din yayi yace "dallah matsa kaban guri azalumin banza ,kai ko za'a yiwa mutane sheda har a maka ina kake da kima da darajan dahar za'a maka haka ae yau taka ta k'are wlh.....

Nan ya k'arasa shiga har gaban kuliya yaje ya duk'a Sannan yace "yamai girma mai shar'a ni nasan me babban lefine banyi niyan bayyana kaina ba amma danaga an kama yaran da basujiba basu ganiba, akan lefin da babu sa hanunun su ciki yasa nace barinzo na wankesu a idon duniya"

"Inaso wannan kotu me adalci da ta bani dama don bada sheda tare a kwakwaran hujjana, ba tare da wani matsala ba"....

Shidai Ss Tafida sakin baki yayi yana kallon ikon Allah, Da sauri Barrt Abbas Ya mik'e tsaya yad'an rusuna yace "yamai girma mai shar'a ina so kotu mai adalci da ta bawa 'wannan bawan Allahan damar fad'an baunde ,yake son fad'a ", da murmushi Jurge Muktar ya gyara zaman gilashin dake fuskar shi yace"kotu ta bashi dama"

Nan Barrt Abbas ya fito yasa PA yayi ranstuwa da 'Allah cewa bazai bad'i komai ba face gaskiya sannan ya fara magana kamar haka....

"Sunana jabir Abubakar ishaq ni d'an asalin garin kano ne, jin an mabaci Abubakar ishaq yasa Ss Tafida zaro ido tare da razana,

mahaifina yasan Ss Tafida sosai kuma yasan amintar su da mahaifin wa innan bayin Allah, ya nuna su malika, ya cigaba da cewa mahaifina tsiran mutuwanshi da mutuwar k'anin mahaifin su Malika sati biyu ne kuma ba kowa bane ya kasheshi face wannan fasik'in kuma azalumin ya nuna Ss Tafida ,cikin zafin nama fadil ya mik'e zeyi rigima Ss Tafida yayi saurin rik'eshi yace barshi,

Ya ciga da cewa shine sanadin mutuwa Iyaye na, mahaifina shine d'an jaridan da yayi niyar taimakon su Malika lokacin da Wannan Azalumin ya lalatawa mahaifiyar su rayuwa, amma da yake shu mugu ne sai ya kashe shi".

" Bazan ta6a mantawa ba ranar litinin ,da misalin k'arfe ukun dare muna kwance a d'aki nida yayata, wadda alokacin bazata wuce she kara 15 ba' a lokacin ni kuma ina k'arami ,amma da wayo na , iyayen mu kuma suna d'aki suma mukaji buga k'ofa kamar zasu fasa k'ofar gidan , da sauri mahaifina yaje bud'e mahaifiya ta kuma' a tsurace ta shigo d'akin mu ta samu duk mun tashi don muma mun tsorata da bugun kofar da suka yi"...

"Nan muka fito falo gaba d'ayan mu muna jiran dawowan baba, kawai mukaji yana salati da sauri mahaifiyata ta 6oyeni cikin wani table, dake falon kafun su shigo tace kuma kar na fito, ina kallo wasu mutane wurin su 7suka shigo kuma da gani duk abokan sane d'aya ya tuso mahaifina da bindiga har tsakar falon suka ce yatata da mamana duk su tsuguna haka kuwa akayi , shi kuma mahaifina buga masa k'asan bindiga ,Sukace shima ya rusuna nan ya rusuna ya d'aga hanayen shi , ina kallo Ss Tafida yazo da wannan bak'ar fuskar tashi kamar na gorilla yace bamu video d'in da kayi nan mahaifina yace wlh bazai basuba sai dai su kashe shi ,sukayi sukayi ya hanasu innarilahi wa inna ilaihi raju'un a idona Ss Tafida ya danna masa bindiga 'a tsakar kansa ya fad'i gurin a muce fad'uwar sace yasa mama kukan kura ta mik'e zata fice suka harbeta' a k'afa ita ma ta fad'i sukayi kanta 'akan ta fad'a musu inda cemaran yake tak'i shine itama suka harbeta a ciki gudun karta tona musu asiri" kuka sosai PA din keyi yacigaba da cewa.

"hakan duk be ishe suba saida suka ketawa yayata haddi dukkansu 7 d'an wanda yasa harsai da ta amsa kiran Allah tsabar wahala kuma 'a idona duk akayi komai duk kuma na gane mutanen da aka tafi dasu, kasa kuka nayi kuma na kasa ihu, haka 'aka zo aka kwashi su aka musu wanka aka kaisu makwancin su, ya zama bani da kowa sai Allah gashi dama bamu san inda yan uwan mahaifina suke ba"...

"Tow kunji labarina , tow tunda wannan rana, na k'ulaci Ss Tafida, da 'abokan sa 'akan saina d'auki *Fansar Abun da sukayi wa family na* tun daga ranar na tsani maza ,kuma na dena tsoran kowa ,

Dalilin da yasa naje gidan Ss Tafida bayan shekaru masu yawa 'a matsayin PA d'inshi don na rama cin mutuncin daya mun"

Yana dariya yace "nasan zakuyi mamakin abunda zan fad'a yanzu, nine MK d'innan da yake kisa gidan Ss Tafida , kuma duk kisan da 'ake a gidan ninakeyi kuma nina kashe Ambsd Rabi da hanuna ,kuma ninayi yink'urin kashe Ss Tafida , wlh danaji cewa be mutuba , ba k'aramin bak'in ciki na shiga ba , nine dai mutumin daya d'auki Fahad kuma insha Allah yau zaku ganshi"...

Yana rufe baki saiga Fahad ya shigo wayyo dad'i , Hajiya na ganinshi da gudu taje ta rungume shi ,nan fa kotu ya k'ara kaurewa da surutu , masu video ko sai d'auka suke, Ss Tafida kam babu abun da yake sai sharara zufa da zaro ido kamar na mujiya....

Jurge Muktar yayi matuk'ar farin cikin ganin d'an nasa 'amma sam yak'i mik'ewa yaje ya sameshi , Malika ma tayi yin k'urin zuwa 'amma fir yan sandan dake kusa dasu ,suka hanata....

Da Jurge Muktar yaga ihu da surutun da 'ake yayi ,yawa da sauri ya buga kundin gaban sa, babu shiri kowa yayi shiru aka cigaba da sauraron k'ara.....

PA ne yacigaba da magana" yamai girma mai shar'a 'ashirye nake da duk wani hukunci dazaku yanke min don dama ninasan bame nisan kwana bane nariga da nasadaukar da rayuwata ma family na , kuma 'alhmdlh burina ya ciki , ashirye nake da kar6an duk hukuncin da zaku yenke min".....

Yanayi yana dariya, yacigaba da cewa" ni nasan nayi kuskure a rayuwa kuma bana fatan mutun yayi hali irin nawa ,nima sai daga baya na gane cewa hakuri Abune mai kyau Anabimuhad yayi gsky da yace duk abun da 'aka mana muxama masu juriya da hakuri akanshi, naso yin hakan tun farko amma idona ya rufe sabida rad'ad'i da zafin abun da 'akamun yasa na kasa ganewa".....

Ya ,yan uwana ina k'ara jadada muku akan mudinga hakuri da duk abunda ya samemu wata rana an tambayi annabi (S. A. W) cewa mene ne Hakuri? Sai Annabi yace ,

Juriya kan bak'in ciki:
Yin raha ga makiyi:
Cire girman kai:
Karb'an uzuri a gurin da kasan babu gaskiya.
Yafiya ga wanda ya cuce ka.. Tow kunga manzan Allah (S. A. W)yayi gsky da yace mudinga hakuri watarana zai zame mana Alkairi,

Laifi kowa ana yi ma sa amma ,masu rauni suke daukar Fansa. Masu karfi su ,suke yafewa Allah yasa kuyi amfani da sak'on da nake son isar muku dashi Ameen

"Bayan PA yagama fad'ar duk abun dazai fad'a , tukun Barrt Abbas ya kalleshi yace ko zaka bamu wata shedar dazai sa wannan kotu mai adalci ta yadda ,da duk abun da ka fad'a ,batare da wasiwasi ko ,kokontow ba?"

Murmushi PA d'in yayi ,yace "ina da kwararan hujojina tare kuma da shedata' yanzu kuma zan fito dasu, memorys na cemars d'in da Malika tasa gidan Ss Tafida, nina kwashe su bayan nayi aika aikan da zanyi ranar ,dicks ma kuma nina daukeshi ,bayan haka ina da recod ,d'in ranar da Ss Tafida akace ya bada ,Aminin shi "...

Barrt Abbas ne yace "tow muna buk'atar ka bamu su don kowa yaji irin cinzarafin da wannan bawan Allah yayi wa ,wainnan bayin Allah " ya nuna inda su malika ke tsaye....

Babu 6ata lokaci PA ya d'auko duka 'abubuwan daya fad'a ya mik'awa Barrt Abbas ,ya k'ar6a ya saka memory din a jikin system ya kunna sannan ya mik'awa kuliya nan kowa yaga zahirin cewa PA shiya kashe Rabi kuma shiyayi yink'urin kashe Ss Tafida ,babu 'abin da ba'a ganiba duk abunda Ss Tafida keyi a gidan shi har ,ranar da Malika ta d'auki takardun company d'inshi duk saida suka gani.....

Mamaki ya cika kowa a gurin barin ma family d'in Ss Tafida ,don basu ta6a tsamanin shi bane bare suyi tunani.....

Haka Barrt Abbas yayi tasawa har yazo kan ranar da Ss Tafida yabada Baban su Malika ,lokacin da 'akasa recod ,d'in ba k'aramin tadawa Ss Tafida hankali yayi ba ,bashi kad'ai ba har Barrt Sunusi saida gabanshi yayi mutuk'ar tashi tare da tawagan Ss Tafida suma duk saida suka razana nan danan Ss Tafida ya fad'a duniyar tunanin irin hukuncin da za'a yanke masa, haka dai duk Barrt Abbas ya gama sawa snn ya koma ya zauna....

Kuliya ,yajima yana wasu yan rubuce -rubuce sai da yakusa kaiwa wurin 1hours, snn ya d'ago ya fara magana kamar haka." lawyan wainda 'ake tuhuma ko kana da 'abun cewa?"

Barrt Sunusi da duk jikinshi yayi sanyi, shima yana tunanin hukuncin da za'a yanke masa , 'a matsayinshi na lawya da 'aka had'a baki dashi don kisa, ya mik'e tsaye yace "yamai girma mai shari'a bani da abun cewa"...

Gyara takardun dake gabanshi kuliya, yayi sannan yayi gyaran murya, yace bari muje break mu dawo idan kuna da 'abun fad'a sai ku fadi bayan mun dawa , ya tashi ya fice haba nan yan jarida sukayo kan Ss Tafida suna masa tambayoyi , mutane kowa ya fara fita.....

Barrt Sunusi kam kasa tashi yayi duk kunya ta isheshi ,haka ma Ss Tafida....

Barrt Abbas da Barrt Minal ne suka nufo inda Barrt Sunusi ke zaune ,da murmushi Barrt Minal tafara cewa"duniya kenan dama 'ance abunda yake baka tsoro, wata rana shi zai baka tausayi.duk mulkin ka,wata rana sai ta mayar da kai kaskantacce.abun da kake ganin Alkhairi ne, wata rana zai iya zama maka sharri.idan kana ganin kafi kowa ,wata rana zakaga wanda ya fika. Duniya fa kenan Barrt Sunusi ko zaka iya tuna furucinka 'a kaina ranar da muka fito a shiga kotu na biyu?"

"ina ,nasaran taka? ae dama 'Allah baya barin hakkin wani don wani yau wagari ya waya?

Waye yaji kunya tow ina me baka shawara 'akan duk abun da zaka 'aikata na rayuwa, ya zama kanayinshi tsakani da 'Allah tow zakaga dede a rayuwan ka," Barrt Sunusi duk yaji abunda Minal ta fad'a kuma ya d'auka shi de bece dasu komai ba har suka gama suka fice ,suka barshi cikin gurin se nadama da ,dana sani yake, shima tashi yayi ya fice...

K'ARFE BIYU DA RABI NA RANA

A ka dawo daga break kutun ya kuma cika sosai don mutane ,sun kuma k'aruwa , Judge Muktar na zaune hannun shi rik'e da pencil sai bin yan kotun yake da kallo, d'aya bayan d'aya har yakai kan Malika yana kallon ta yaga itama shi take kallo , murmushi yayi mata me cike da jin dad'i ,itama ta mayar masa, snn ya d'aga dubanshi daga gareta ya koma kan Barrt Sunusi ya ce" lawyan wainda suke k'ara kow akwai abun da zaku ce?" Nan Barrt Sunusi ya girgiza kai Alamar a'a , nan ya tmby su Barrt Abbas ma ko suna da 'abun fad'a suka ce a'a.....

Kallon Ss Tafida yayi fuska 'a d'aure yace "Tafida duk kaji abunda 'aka fad'a 'a kanka kow ? yanzu duk abubuwan da kayi meya k'areka dashi ya kake ji yanzu?".....

babu abin dake shinfid'e a fuskar Ss Tafida sai kunyi ,kuma duk wanda ya ganshi yasan yana cike da tsan-tsar nadama ,be iya cewa da 'alk'ali komai ba...

Shiko Judge muktar duk'ufa tayi ya fara rubutu me tsahon gaske lokaci guda kotun yayi tsi-tsit babu k'aran dake tashi saiyan magan ganun mutane k'asa -k'asa,

Bayan shud'ewan wasu lokaci Alk'ali ya d'ago tare da gyara takardun gaban shi, yana mai cigaba da kallon jama'ar dake zaune gaban shi, yafara jawabi kamar haka.

Ina so kowa ya nutsu ya saurari abunda zance ni justice Muktar Garba, zan yanke hunkunci tsakanin Alhaji Sulaiman Salisu Tafida Dake k'aran family d'in Alhaji Salisu Nera ,yad'an gyara zamansa yace..

"Wannan kotu me Adalci ta kama Alhaji Tafida ' da laifin kisa wanda kotu ,ta ,tabbatar da hakan kuma tare da kwararan hujojin ta gamsasu, saboda haka, kotu zataci taranshi na nera miliyan biyar, jabir kayi k'o k'ari dahar ka iya bayyana kanka, duba da rashin wahalar damu dabayi ba, kotu ta yanke maka hukunci zaman gidan yari na tsahon shekara biyar tare da cinka taran nera miliyan d'aya bisa wahalan da 'akasa 'wainnan yara sukayi kai kuma Alhaji Tafida kotu ta yanke maka hukuncin life in prison tare da taran naira miliyan biyar kacal, "

Sai daya d'an numfasa ya k'ara da cewa Barrt Sunusi kuma idan angama shari'a zaka karb'i hukuncin ka bisa dede da lefinka ,don masu hali irin naka suma su gyara..

A k'arshe yace me k'ara da wanda 'ake k'ara suna da damar daga shari'ah idan hukuncin bai gamshe suba . ya buga kundin gabanshi ya harhad'a kayanshi ya mik'e ya fice,

Bayan fitar Alk'ali kotun ta kid'ime da hayaniyi su Nabiha, Noor Aunty Fatima babu abunda suke sai kuka da 'Allah wade, da hali irin na mahaifin su,

Ikon Allah yau ga Ss Tafida yana k'wala 'A lalle yayi nadama , Malika ,kow kasa koda motsi tayi tsabar farinciki ,Barrt Minal ce ta nufo inda take ta mik'a mata hannun tana murmushi, tace "CONGRATULATIONS malika you are free now Allah ya kare gaba"

Wani murna da farin ciki Malika ta tsunci kanta ciki ,ba shiri ta rungume Minal tana cewa"Tnx four your help Barrt Minal Allah ya biyaki da gidan Aljannan " murmushi minal tayi tace "Ameen Malika nizan wuce bauchi yau" tow Allah ya kiyaye hanya ki gaishe min da Barrt Faty insha Allahu zan kawo miki ziyara"cewar Malika , Minal tace "insha Allahu zataji natafi kar nayi dare sai kinzo"nan sukayi salama....

Fitowa su malika sukayi daga cikin kotun kowa sai congrat yake musu, yan jarida ko sai binsu suke , Ss Tafida ma 'anfito dasu ansasu amota sunwuce gidan yari...

Su Malika na fitowa Taga Fahad kasa 6oye farin cikin da take ciki tayi saurin taje ta rungumeshi tana "welcome home yayana i missed you so much Alhmdulh tunda Allah ya dawo min dakai lfy, i love you to the moon &back to infinity nd beyond forever nd ever".

Da sauri Fahad ya saketa yana kallonta yace "mekikace Diyana ?"

Sai alokacin taji kunya ta kamata don ita duk batasan ta fad'a ba ,kulle idon ta tayi wai ita kunya😀 tace "babu abinda nace yayana kadena cemin Diyana sunana Malika😊tad'anyi murmushi ta gudu gurin su Hajiya don kunyarshi take ji.....

☺😊☺😊
[3/31, 10:49 PM] Dija waziri: □□□□□□□□□
FANSA

REVENGE
□□□□□□□□□

Story /writing by dija_waziri

this page goes to all masoyan Fansa thank all for your love care, nd support❤❤

LAST PAGE

□

(P. W. F)

Page
96&100

BAYAN SHEKARA GOMA SHA D'AYA

Abubuwa da dama sun faru, ciki harda auren su Malika, dasu Nabiha wanda 'a halin yanzu harda yaran su inda Malika ta auri Fahad, Zahra kuma ta auri Barrt Abbas , Ahlam ma tasamu wani mai sonta ta aura...

Ss Tafida kuwa Allah yayi masa rasuwa sakamakon ciwan zuciya daya 'adabeshi da kuma tsantsar wahala dayake sha 'a gidan yari ,

Kausar kuma har tayi gradution a jami'ar bayaro dake garin kano, a fannin lafiya..

Yaran Ss Tafida sunyi nadama sosai kuma yanzu sunzama cikin family d'in Judge Muktar, Hajiya khadija ta samu ,miji tayi aure

Tow a gurguje barimu lek'a family house d'in Su Malika, gidane k'aton gaske Judge Muktar yagina ,na 'alfarma duk wanda yaga ,gidan kasan gidan atajirin mai kud'ine, wanda nera ta zauna masa , wasu fararen yara da bak'ake na gani wurin su shida sai wasan guje guje suke a farfajiyan gidan gwanin ban shi'awa, ga dukkan alamu jikokin gidanne....

Wasu nagani mace da namiji farare sunyo wurin gardin d'in gidan, suna guje guje macen bazata wuce shekara 5 ba shi kuma namijin shekara 7 kuma kamansu d'aya da Malika hakan yasa na gane cewa yaran tane su...

Cikin gidan 'na k'arasa kai abunda nagani ya balain burgeni , su Malikane zaune cikin wani k'aton falow ko wacce kusa da mijinta, suna hira cikin raha da jin dad'i Judge Muktar da Hajiya suna kan kujera sai murmushi suke , Hajiya sanye da tabarau a idon ta alamomin tsufa duk sun bayyana a shinfid'e a fuskar ta...

Malika na hango sai zabgawa Fahad shawo6a take sai kace wata beby😄 had'a ido mukayi da ita na d'aga mata hannu fuskata d'auke da fara'a ,nace "Happy new life "da k'arfi wanda yasa yan falon d'agowa gabad'aya suka zubamin ido, da murmushi ,shinfid'e a fuskarta ,tace "thank you " naga ta cilomin wani abu da sauri na cafe naga 'ashe mukulin motane😂 wai😹 ni dija bakina kasa rufuwa yayi don murna bansan sanda na yadda biron hanuna ba☺....

Tow yan uwa anan na kawo k'arshen wannan littafi.. Anan nakece daku

ALHAMDULILLAH

Godiya ta, tabata ga Allah mai kowa mai komai daya bani ikon, kawo k'arshen wannan labarin kuskuren da nayi Allah ka yafemin Allah kasa mutane su amfana da 'abun dake ciki Ameen...

Jijina gareki yar uwa rabun jiki miemie waziri nagode da taimakonki da kuma shawarinki Allah yabar zumunci ya barmu tare

Na gaishe ku yan uwana

Sadiya waziri
Nana waziri
Miemie waziri
Walida waziri
Ina kaunarku sosai Allah ya barmu tare😍😍😘

Ban manta dakuba k'awayena

Fatima uba suleman
Ummi muhd tahir
Amina sukairaj
Rahama shitu
Sadiya isa dauda
Ina kaunarku aduk inda kuke❤😘

Kuna raina k'awayen arziki

Faty azland my mummy😘
Jannat (k'awata ,ta kaina)
Class feedor
Zee yabour(ina Alfahari dake)
Sis Ayusha ilyasu
First lady
Nicedai
Neeratlurv(my bsty)😘

Rookiy
Sajna
Mss Aisha
Husna bh
Ummi Hambali
Maman ihsan
Hafsat musa
Miss hafsey
Maman useey
Miss xoxo
Waliyya muh'd
Zara bukar
Aisha abbakar(meera)
Da sauran wanda ban ambataba duk kuna raina ina sonku😍

Jinjina gareku yan p.w.f nagode da kaunarku da irin kulawar da kuke nuna min hakik'a muna k'aruwa sosai Allah ya biyaku da gidan Aljanna ya k'ara had'a kanmu ❤

Ina Alfahari daku yan group d'ina dija waziri novels Allah ya barmin ku😊😘

Jinjina gareku
Jannat Novel
Musan juna O. H. W
Zara bukar novel
Taskar lubee mai tafsir
M sultan novel
Novel only
Novels loves
Online hausa writer feedor online novels
Walida waziri novel
Da duk wanda ban samu daman ambata ba duk ina muku fatan Alkairi😊

Ban manta dakuba reads daku nake tink'aho ina Alfahari daku nagode ,da irin soyayyar da kuke nuna min da bazarku nake rawa ina muku fatan Aljairi

Dija_waziri na kyaunarku sosai❤

Annan nake cewa daku ma'a salam ,sai mun had'u daku cikin sabon novel d'ina ,wanda zai zo muku nan bada jimawaba inde muna raye salamu Alaikum😊
😊